الجزء ١٦ الحزب ٣١

۞ قَالَ أَلَمۡ أَقُل لَّكَ إِنَّكَ لَن تَسۡتَطِيعَ مَعِيَ صَبۡرٗا ٧٥ قَالَ إِن
سَأَلۡتُكَ عَن شَيۡءِۭ بَعۡدَهَا فَلَا تُصَٰحِبۡنِيۖ قَدۡ بَلَغۡتَ مِن لَّدُنِّي عُذۡرٗا
٧٦ فَٱنطَلَقَا حَتَّىٰٓ إِذَآ أَتَيَآ أَهۡلَ قَرۡيَةٍ ٱسۡتَطۡعَمَآ أَهۡلَهَا فَأَبَوۡاْ
أَن يُضَيِّفُوهُمَا فَوَجَدَا فِيهَا جِدَارٗا يُرِيدُ أَن يَنقَضَّ فَأَقَامَهُۥۖ
قَالَ لَوۡ شِئۡتَ لَتَّخَذۡتَ عَلَيۡهِ أَجۡرٗا ٧٧ قَالَ هَٰذَا فِرَاقُ بَيۡنِي
وَبَيۡنِكَۚ سَأُنَبِّئُكَ بِتَأۡوِيلِ مَا لَمۡ تَسۡتَطِع عَّلَيۡهِ صَبۡرًا ٧٨ أَمَّا
ٱلسَّفِينَةُ فَكَانَتۡ لِمَسَٰكِينَ يَعۡمَلُونَ فِي ٱلۡبَحۡرِ فَأَرَدتُّ أَنۡ
أَعِيبَهَا وَكَانَ وَرَآءَهُم مَّلِكٞ يَأۡخُذُ كُلَّ سَفِينَةٍ غَصۡبٗا ٧٩ وَأَمَّا
ٱلۡغُلَٰمُ فَكَانَ أَبَوَاهُ مُؤۡمِنَيۡنِ فَخَشِينَآ أَن يُرۡهِقَهُمَا طُغۡيَٰنٗا
وَكُفۡرٗا ٨٠ فَأَرَدۡنَآ أَن يُبۡدِلَهُمَا رَبُّهُمَا خَيۡرٗا مِّنۡهُ زَكَوٰةٗ وَأَقۡرَبَ
رُحۡمٗا ٨١ وَأَمَّا ٱلۡجِدَارُ فَكَانَ لِغُلَٰمَيۡنِ يَتِيمَيۡنِ فِي ٱلۡمَدِينَةِ
وَكَانَ تَحۡتَهُۥ كَنزٞ لَّهُمَا وَكَانَ أَبُوهُمَا صَٰلِحٗا فَأَرَادَ رَبُّكَ أَن
يَبۡلُغَآ أَشُدَّهُمَا وَيَسۡتَخۡرِجَا كَنزَهُمَا رَحۡمَةٗ مِّن رَّبِّكَۚ
وَمَا فَعَلۡتُهُۥ عَنۡ أَمۡرِيۚ ذَٰلِكَ تَأۡوِيلُ مَا لَمۡ تَسۡطِع عَّلَيۡهِ صَبۡرٗا ٨٢
وَيَسۡـَٔلُونَكَ عَن ذِي ٱلۡقَرۡنَيۡنِۖ قُلۡ سَأَتۡلُواْ عَلَيۡكُم مِّنۡهُ ذِكۡرًا ٨٣



**(75) Khadir ya cewa Annabi Musa (A.S): "Ashe ba na riga na faxa maka cewa: Lallai – Kai Musa - ba zaka tava iya haquri da abin da zan aiwatar na al'amura na ba?!".**

**(76) Sai Annabi Musa (A.S) ya ce: "Idan na sake tmbayarka wani abu bayan wannan, to ka rabu da ni, don in haka ya sake faruwa, to lallai ka kai matuqar da za a yi maka uzuri akan rabuwa da ni, saboda na sava umarninka kenan har sau uku".**

**(77) Sai suka ci gaba da tafiya, har suka isa wajen wasu mutanen wata alqarya, suka nemi abinci daga wurinsu, sai mutanen alqaryar suka qi su basu wani abinci, suka hana su haqqin baquntaka. Ana haka sai suka ga wata katanga a karkace, tana shirin faxuwa qasa ta rushe, sai Khadir ya gyara ta, ya tayar da ita, har ta daidaita a tsaye. Sai Annabi Musa (A.S) ya ce wa Khadir: "Da ka ga damar karvar lada akan wannan gyara da ka yi, ai da ka karva, saboda muna buqata, tunda sun qi saukar mu".**

**(78) Sai Khadir ya cewa Annabi Musa (A.S): "Wannan katsalandan dangane da rashin karvar lada akan daidaita katanga, shi ne wurin rabuwa tsakanina da kai. Amma zan yi maka bayanin abin da ka kasa haquri a kai, cikin abubawan da na yi, waxanda ka gani".**

**(79) Shi dai jirgin ruwan da ka yi min inkarin huda shi, to ya kasance na wasu masu rauni ne, talakawa, suna aiki da shi a cikin teku, ba zasu iya kare shi ba, sai na so ya zama yana da wani aibi, saboda hudawar da na yi masa, saboda kar wani sarki, da yake a gaba, wanda yake qwace duk wani jirgin ruwa mai kyau da qarfi a wurin masu shi, ya qyale mai aibu, ya qwace musu na su jirgin".**

**(80) "Amma yaron da ka yi min inkari kashe shi kuwa, to iyayensa sun kasance muminai ne, shi kuma ya kasance a kafiri ne a ilimin Allah, sai muka ji tsoron in ya balaga, yana iya tirsasa su akan kafirce wa Allah, da qetare iyakokinsa, saboda tsananin soyayyarsu gare shi, ko kuma saboda tsananin buqatuwarsu gare shi".**

**(81) Sai muka yi nufin Allah ya musanya musu, da wani yaro, wanda zai fi musu alheri wajen addini da nagarta, da tsarkaka daga zunubi, kuma wanda zai fi kusa da nuna jinqai ga iyayensa sama da wannan".**

**(82) Amma katangar da na gyara, har ka yi min inkarin gyaranta kuwa, to ta wasu qananan yara ne guda biyu, a alqaryar da muka zo cikinta, mahaifinsu ya riga ya rasu. Kuma a qasan katangar akwai dukiyarsu a binne, kuma babansu ya kasance mutumin kirki ne. Shi ne sai Ubangijinka – Ya kai Musa- ya yi nufin su kai shekarun hankali, su girma, har su fitar da dukiyarsu dake binne a qasan katangar, don da katangar ta faxi yanzu, to da dukiyar tasu zata bayyana, kuma ana iya rasa ta. Wannan shirin ya kasance jin qai ne daga wurin Ubangijinsu a gare su. Ba na yi shi da tunani na ba ne. Wannan shi ne bayanin abin da ka qasa haquri a kansa".**

**(83) Mushirikai da Yahudawa suna tambayarka – Ya kai wannan Manzo- don su jarraba ka akan labarin Zulqarnaini, to ka ce musu: "Da sannu zan baku wani vangare na labarinsa, wanda zaku dauki izina, kuma ku wa'azantu da shi".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Wajabcin yin taka-tsantsan da tabbatarwa, da rashin gaggawa wajen yin hukunci akan wani abu.**

**2 - Hukunce hukuncen abubuwa suna gudana ne akan zahirinsu, kuma akan zahiri ne ake jingina hukunce hukuncensu na duniya, a cikin dukiyoyi da jini da sauransu. 3 - Ana tunquxe babban sharri ta hanyar aikata qaramin sharri, kuma ana la'akari da mafi girman maslaha guda biyu, ta hanyar kawar da qaramin cikinsu.**

**4 - Ya dace kar aboki ya rabu da abokinsa, ya raba gari da shi, har sai bayan ya gargaxe shi, ya kafa masa hanzari.**

**5 - Yin ladabi ga Allah cikin lafuzza, ta hanyar jingina alheri zuwa gare shi, da rashin jingina sharri zuwa gare shi.**

**6 - Bawa na qwarai Allah yana kare shi a karan kansa, da kuma zuriyarsa.**

إِنَّا مَكَّنَّا لَهُۥ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَءَاتَيۡنَٰهُ مِن كُلِّ شَيۡءٖ سَبَبٗا ﴿٨٤﴾ فَأَتۡبَعَ سَبَبًا
﴿٨٥﴾ حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغَ مَغۡرِبَ ٱلشَّمۡسِ وَجَدَهَا تَغۡرُبُ فِي عَيۡنٍ حَمِئَةٖ
وَوَجَدَ عِندَهَا قَوۡمٗاۗ قُلۡنَا يَٰذَا ٱلۡقَرۡنَيۡنِ إِمَّآ أَن تُعَذِّبَ وَإِمَّآ أَن تَتَّخِذَ
فِيهِمۡ حُسۡنٗا ﴿٨٦﴾ قَالَ أَمَّا مَن ظَلَمَ فَسَوۡفَ نُعَذِّبُهُۥ ثُمَّ يُرَدُّ إِلَىٰ رَبِّهِۦ
فَيُعَذِّبُهُۥ عَذَابٗا نُّكۡرٗا ﴿٨٧﴾ وَأَمَّا مَنۡ ءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحٗا فَلَهُۥ جَزَآءً
ٱلۡحُسۡنَىٰۖ وَسَنَقُولُ لَهُۥ مِنۡ أَمۡرِنَا يُسۡرٗا ﴿٨٨﴾ ثُمَّ أَتۡبَعَ سَبَبًا ﴿٨٩﴾ حَتَّىٰٓ
إِذَا بَلَغَ مَطۡلِعَ ٱلشَّمۡسِ وَجَدَهَا تَطۡلُعُ عَلَىٰ قَوۡمٖ لَّمۡ نَجۡعَل لَّهُم مِّن
دُونِهَا سِتۡرٗا ﴿٩٠﴾ كَذَٰلِكَۖ وَقَدۡ أَحَطۡنَا بِمَا لَدَيۡهِ خُبۡرٗا ﴿٩١﴾ ثُمَّ
أَتۡبَعَ سَبَبًا ﴿٩٢﴾ حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغَ بَيۡنَ ٱلسَّدَّيۡنِ وَجَدَ مِن دُونِهِمَا قَوۡمٗا
لَّا يَكَادُونَ يَفۡقَهُونَ قَوۡلٗا ﴿٩٣﴾ قَالُواْ يَٰذَا ٱلۡقَرۡنَيۡنِ إِنَّ يَأۡجُوجَ
وَمَأۡجُوجَ مُفۡسِدُونَ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَهَلۡ نَجۡعَلُ لَكَ خَرۡجًا عَلَىٰٓ أَن
تَجۡعَلَ بَيۡنَنَا وَبَيۡنَهُمۡ سَدّٗا ﴿٩٤﴾ قَالَ مَا مَكَّنِّي فِيهِ رَبِّي خَيۡرٞ فَأَعِينُونِي
بِقُوَّةٍ أَجۡعَلۡ بَيۡنَكُمۡ وَبَيۡنَهُمۡ رَدۡمًا ﴿٩٥﴾ ءَاتُونِي زُبَرَ ٱلۡحَدِيدِۖ حَتَّىٰٓ إِذَا سَاوَىٰ
بَيۡنَ ٱلصَّدَفَيۡنِ قَالَ ٱنفُخُواْۖ حَتَّىٰٓ إِذَا جَعَلَهُۥ نَارٗا قَالَ ءَاتُونِيٓ أُفۡرِغۡ عَلَيۡهِ
قِطۡرٗا ﴿٩٦﴾ فَمَا ٱسۡطَٰعُوٓاْ أَن يَظۡهَرُوهُ وَمَا ٱسۡتَطَٰعُواْ لَهُۥ نَقۡبٗا ﴿٩٧﴾



(84) Haqiqa mun tabbatar da shi a bayan qasa, mun bashi komai da yake da alaqa da abin da yake nema, don ya zamar masa hanyar da zai cimma burinsa.

(85) Sai ya yi riqo da abin da muka bashi, na hanyoyi da abubuwa don isa zuwa ga abin da yake nema, don haka sai ya yi yamma.

(86) Ya yi ta tafiya a bayan qasa, har sai da ya isa qarshen qasa ta vangaren yamma, inda rana ke faxuwa, sai ya ga kamar rana tana faxuwa a cikin wani idon ruwa mai zafi, mai baqin tavo, kuma ya samu wasu mutane kafirai a wajen mafaxar ranar. Sai muka ce masa, muna ba shi zavi: “Ya kai Zulqarnaini, imma ka azabta waxannan mutane, da kisa ko da waninsa, ko kuma ka kyautata musu”.

(87) Sai Zulqarnaini ya ce: “Amma duk wanda ya yi wa Allah shirka, ya kuma zarce akan hakan, bayan mun kira shi zuwa ga bautar Allah shi kaxai, to zamu yi masa uquba da kisa a nan duniya, sannan kuma za a komar da shi zuwa ga Ubangijinsa a ranar alqiyama, ya yi masa azaba mai tsananin muni”.

(88) “Amma duk wanda ya yi imani da Allah a cikinsu, kuma ya yi aiki nagari, to yana da Aljanna a matsayin sakamako daga Ubangijinsa akan imaninsa, da aikinsa nagari. Kuma da sannu zamu faxa masa zance mai sauqi da tausayi cikin lamarinmu”.

(89) Sannan ya bi wata hanya savanin hanyarsa ta farko ya nufi mahudan rana.

(90) Ya yi ta tafiya, har sai da ya kai wurin da rana take vullowa, sai ya ga cewa rana tana vullowa ne a wurin wasu mutane, waxanda bamu saka musu wani wani abu, wanda zai kare su daga zafin rana, na gidaje ko inuwar bishiyoyi ba. (91) Haka lamarin Zulqarnaini ya ke. Lallai iliminmu ya kewaye abin da yake da shi, na qarfi da mulki, dalla dalla.

(92) Sannan kuma ya sake bin wata hanya, savanin hanyoyin can guda biyu na farko, yana mai tafiya tsakanin mahudar rana da mafaxarta. (93) Ya yi ta tafiya, har sai da ya isa wani wuri tsakanin duwatsu guda biyu, sai ya samu wasu mutane a wurin, waxanda ko kusa ba sa fahimtar yaren wasu, wanda ba na su ba.

(94) Sai suka ce: “Ya kai Zulqarnaini, lallai fa Yajuj da Majuju (suna nufin wasu al'ummu guda biyu masu girma daga cikin ‘ya’yan Adam) mavarnata ne a bayan qasa, saboda abin da suke aikatawa na kisa da sauransu. Shin mu baka lada na dukiya, don ka saka wata katanga tsakanin mu da su?”.

(95) Sai Zulqarnaini ya ce: “Abin da Ubangijina ya azurtani da shi, na qarfi da mulki, ya fi min alheri akan abin da zaku bani na dukiya. Ku dai, ku taimaka mini da mutane (ma'aikata) da kayan aiki, zan saka shamaki tsakaninku da su”. (96) Ku kawo min guntayen qarfe. Sai suka kawo masa, sai ya fara gini da su, a tsakanin duwatsun guda biyu, har sai da tsawon ginin ya yi daidai da duwatsun, sai ya ce wa ma'aikatan nan: “Ku kunna wuta a kan waxannan guntayen qarafunan, har sai da guntayen qarfen suka yi ja- jawur, sai ya ce: “Ku kawo mini narkakken tagulla in zuba a kansa”. (97) Yajuju da Majuju baza su iya tsallake shi ba, saboda tsayinsa, kuma ba za su iya huda shi daga qasan shi ba, saboda qarfinsa.

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

1 - Zulqarnaini xaya ne daga cikin sarakuna muminai, waxanda suka mallaki duniya, suka yi sarauta a kan mutanenta, saboda Allah ya ba shi mulki mai yalwa, kuma ya ba shi hikima da kwarjini da ilimi mai amfani.

2 - Yana daga cikin wajibin Sarki ko Shugaba ya tashi tsaye wajen bayar da kariya ga mutane cikin tsaron gidajensu, da gyara musu iyakokinsu daga cikin dukiyansu. 3 - Mutanen kirki da masu ikhlasi suna kwaxayin su aiwatar da ayyuka, domin neman yardar Allah.

قَالَ هَٰذَا رَحْمَةٌ مِّن رَّبِّي ۖ فَإِذَا جَاءَ وَعْدُ رَبِّي جَعَلَهُ دَكَّاءَ ۖ وَكَانَ وَعْدُ رَبِّي
حَقًّا ﴿٩٨﴾ ۞ وَتَرَكْنَا بَعْضَهُمْ يَوْمَئِذٍ يَمُوجُ فِي بَعْضٍ ۖ وَنُفِخَ فِي الصُّورِ الحزب ٣١
فَجَمَعْنَاهُمْ جَمْعًا ﴿٩٩﴾ وَعَرَضْنَا جَهَنَّمَ يَوْمَئِذٍ لِّلْكَافِرِينَ عَرْضًا ﴿١٠٠﴾
الَّذِينَ كَانَتْ أَعْيُنُهُمْ فِي غِطَاءٍ عَن ذِكْرِي وَكَانُوا لَا يَسْتَطِيعُونَ سَمْعًا
﴿١٠١﴾ أَفَحَسِبَ الَّذِينَ كَفَرُوا أَن يَتَّخِذُوا عِبَادِي مِن دُونِي أَوْلِيَاءَ ۚ إِنَّا
أَعْتَدْنَا جَهَنَّمَ لِلْكَافِرِينَ نُزُلًا ﴿١٠٢﴾ قُلْ هَلْ نُنَبِّئُكُم بِالْأَخْسَرِينَ أَعْمَالًا
﴿١٠٣﴾ الَّذِينَ ضَلَّ سَعْيُهُمْ فِي الْحَيَاةِ الدُّنْيَا وَهُمْ يَحْسَبُونَ أَنَّهُمْ يُحْسِنُونَ
صُنْعًا ﴿١٠٤﴾ أُولَٰئِكَ الَّذِينَ كَفَرُوا بِآيَاتِ رَبِّهِمْ وَلِقَائِهِ فَحَبِطَتْ
أَعْمَالُهُمْ فَلَا نُقِيمُ لَهُمْ يَوْمَ الْقِيَامَةِ وَزْنًا ﴿١٠٥﴾ ذَٰلِكَ جَزَاؤُهُمْ جَهَنَّمُ
بِمَا كَفَرُوا وَاتَّخَذُوا آيَاتِي وَرُسُلِي هُزُوًا ﴿١٠٦﴾ إِنَّ الَّذِينَ آمَنُوا وَعَمِلُوا
الصَّالِحَاتِ كَانَتْ لَهُمْ جَنَّاتُ الْفِرْدَوْسِ نُزُلًا ﴿١٠٧﴾ خَالِدِينَ فِيهَا
لَا يَبْغُونَ عَنْهَا حِوَلًا ﴿١٠٨﴾ قُل لَّوْ كَانَ الْبَحْرُ مِدَادًا لِّكَلِمَاتِ رَبِّي لَنَفِدَ
الْبَحْرُ قَبْلَ أَن تَنفَدَ كَلِمَاتُ رَبِّي وَلَوْ جِئْنَا بِمِثْلِهِ مَدَدًا ﴿١٠٩﴾ قُلْ إِنَّمَا
أَنَا بَشَرٌ مِّثْلُكُمْ يُوحَىٰ إِلَيَّ أَنَّمَا إِلَٰهُكُمْ إِلَٰهٌ وَاحِدٌ ۖ فَمَن كَانَ يَرْجُو
لِقَاءَ رَبِّهِ فَلْيَعْمَلْ عَمَلًا صَالِحًا وَلَا يُشْرِكْ بِعِبَادَةِ رَبِّهِ أَحَدًا ﴿١١٠﴾



**(98) Zulqarnaini ya ce: "Wannan katangar rahama ce dagaUbangijina, zai hana Yajuju da Majuju varna a bayan qasa. Amma idan lokacin da Allah ya qayyade na fitowarsu ya yi, gabanin tashin alqiyama, to zai mayar da ita, ta zama daidai da qasa. Alqawarin Allah na daidaita ta da qasa, da kuma fitowar Yajuju da Majuju tabbatacce ne zai faru, babu savawa cikin sa.**

**(99) Muka qyale wasu halittu a qarshen zamani suna fagamniya, suna cuxanya da juna. Kuma za yi busa cikin qaho, sai mu tara halittu gaba xaya, domin a yi musu hisabi da sakamako.**

**(100) Kuma zamu bijiro da Jahannama ga kafirai, bijirowar da babu rufi a cikinta, don su gan ta qiri- qiri. (101) Zamu bijiro da ita ga kafiran da sun kasance masu makanta daga ambaton Allah a gidan duniya, saboda a abin da yake kan idanunsu na shamaki mai hana su yin hakan. Kuma sun kasance basa iya jin ayoyin Allah, ji na karva da yarda.**

**(102) Shin waxanda suka kafirce wa Allah, suna zaton za su mayar da bayina Mala'iku da Manzanni da Shaixanu abubuwan bautawa koma bayana?!. Lallai mun yi wa kafirai tanadin wutar Jahannama a matsayin masaukinsu, da zasu zauna a cikinsa.**

**(103) Ka ce – Ya kai wannan Manzo-: "Shin – Ya ku mutane - kuna son mu baku labarin waxanda suka fi kowa hasarar ayyukansu a cikin mutane?".**

**(104) Sune waxanda a ranar lahira zasu ga ayyukansu da suka yi a gidan duniya duka sun vaci, alhali su suna zaton su masu kyautata ayyukansu ne, suna ganin za su amfana da ayyukansu, alhali kuwa abin da ya faru savanin haka yake.**

**(105) Waxannan sune waxanda suka kafirce wa ayoyin Ubangijinsu masu nuna kaxaitakarsa, kuma suka kafirce wa saduwa da shi, sai ayyukansu suka lalace, saboda kafircirsu, don haka basu da wata qima a wurin Allah a ranar alqiyama. (106) Sakamakon da aka tanadar musu shi ne Wutar Jahannama, saboda kafircinsu, da yadda suka xauki ayoyina da abin da aka saukar musu da shi a matsayin abin izgili.**

**Bayan Allah ya ambaci sakamakon kafirai, sai kuma ya ambaci sakamakon muminai, ya ce:**

**(107) Lallai waxanda suka yi imani, kuma suka aikata ayyuka nagari to Aljannar Firdausi wadda take mafi xaukakar Aljanna, ita ce mazauninsu, domin girmamawa a gare su.**

**(108) Zasu zauna a cikinta har abada, ba za su nemi canji daga cikinta ba, domin babu wani sakamakon da ya yi kusa da ita.**

**(109) Ya kai Wannan Manzo ka ce: "Haqiqa kalmomin Ubangijina suna da yawa. Da a ce ruwan teku zai zama tauwadar da za a rubuta su da shi, to da ruwan tekun ya qare, kafin kalmomin Ubangiji Maxaukakin Sarki su qare, ko da kuwa zamu kawo wasu tekuna, da suma sun qare.**

**(110) Ya kai wannan Manzo ka ce: "Ni fa mutum ne ne kamarku, ana mini wahayi, cewa abin bautawar ku da cancanta da gaskiya, abin bauta ne guda xaya, ba shi da abokin tarayya, kuma shi ne Allah. Duk wanda yake jin tsoron haxuwarsa da Ubangijinsa to ya aikata aiki, wanda ya dace da shari'arsa, ya tsarkake zuciyarsa ga Ubangijinsa, kuma kar ya kar ya haxa da wani cikin bautar Ubangijinsa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Tabbatar da tashin alqiyama da taron alqiyama, inda za a tattaro mutane da aljannu a farfajiyar alqiyama, ta hanyar busa qaho na biyu. 2 - Mafi tsananin hasara cikin mutane a ranar alqiyama su ne waxanda aikinsu ya vace a duniya, amma suna zaton cewa suna kyautata aiki ne, cikin bautar wani koma bayan Allah.**

**3 - Ba zi yiwu a qididdige kalmomin Allah Maxaukakin Sarki, da iliminsa da hikimarsa da sirrinsa ba, ko da kuwa koguna da tekuna da ire-irensu, ba iyaka, zasu zama tauwada da za a rubuta su, da su.**

سُورَةُ مَرۡيَمَ

آياتها ٩٨ — ترتيبها ١٩

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

كٓهيعٓصٓ ١ ذِكۡرُ رَحۡمَتِ رَبِّكَ عَبۡدَهُۥ زَكَرِيَّآ ٢ إِذۡ
نَادَىٰ رَبَّهُۥ نِدَآءً خَفِيّٗا ٣ قَالَ رَبِّ إِنِّي وَهَنَ ٱلۡعَظۡمُ مِنِّي
وَٱشۡتَعَلَ ٱلرَّأۡسُ شَيۡبٗا وَلَمۡ أَكُنۢ بِدُعَآئِكَ رَبِّ شَقِيّٗا
٤ وَإِنِّي خِفۡتُ ٱلۡمَوَٰلِيَ مِن وَرَآءِي وَكَانَتِ ٱمۡرَأَتِي
عَاقِرٗا فَهَبۡ لِي مِن لَّدُنكَ وَلِيّٗا ٥ يَرِثُنِي وَيَرِثُ مِنۡ
ءَالِ يَعۡقُوبَۖ وَٱجۡعَلۡهُ رَبِّ رَضِيّٗا ٦ يَٰزَكَرِيَّآ إِنَّا
نُبَشِّرُكَ بِغُلَٰمٍ ٱسۡمُهُۥ يَحۡيَىٰ لَمۡ نَجۡعَل لَّهُۥ مِن قَبۡلُ سَمِيّٗا
٧ قَالَ رَبِّ أَنَّىٰ يَكُونُ لِي غُلَٰمٞ وَكَانَتِ ٱمۡرَأَتِي عَاقِرٗا
وَقَدۡ بَلَغۡتُ مِنَ ٱلۡكِبَرِ عِتِيّٗا ٨ قَالَ كَذَٰلِكَ قَالَ
رَبُّكَ هُوَ عَلَيَّ هَيِّنٞ وَقَدۡ خَلَقۡتُكَ مِن قَبۡلُ وَلَمۡ تَكُ
شَيۡـٔٗا ٩ قَالَ رَبِّ ٱجۡعَل لِّيٓ ءَايَةٗۖ قَالَ ءَايَتُكَ أَلَّا
تُكَلِّمَ ٱلنَّاسَ ثَلَٰثَ لَيَالٖ سَوِيّٗا ١٠ فَخَرَجَ عَلَىٰ قَوۡمِهِۦ مِنَ
ٱلۡمِحۡرَابِ فَأَوۡحَىٰٓ إِلَيۡهِمۡ أَن سَبِّحُواْ بُكۡرَةٗ وَعَشِيّٗا ١١



# Suratu Maryam

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**: Bayanin yadda Allah yake nuna rahamarsa ga waliyyansa, kamar basu kyautar xa nagartacce, da bayanin Allah Maxaukakin Sarki ya tsarkaka daga xa, da mataimaki, don mayar da martani ga maqaryata.**

## Tafsir:

**(1) Kaf, Ha, Yaa, Ain, Sad: Bayani ya gabata dangane da ire-iren waxannan haruffa a farkon Suratul Baqara.**

**(2) Wannan ambaton rahamar Ubangijinka ne ga bawansa Annabi Zakariyya, muna baka labarin abin da ya faru don xaukar izna daga cikinsa.**

**(3) Yayin da ya kira Ubangijinsa tsarki ya tabbata a gare shi, kira a voye, don yafi kusa ga amsawa.**

**(4) Ya ce: Ya Ubangijina. Lallai qasusuwa na sun yi rauni, kuma kaina ya yi furfura da yawa, amma ban kasance mai tavewa cikin addu'ata a gare ka ba. Duk lokacin da na roqe ka kana amsa mini.**

**(5) Haqiqa ina jin tsoron kar dangi na su kasa tsayar da haqqin addini bayan mutuwa ta, saboda shagaltuwarsu da duniya, kuma ga mata ta ta kasance bakarariya, ba ta haihuwa, don haka ka yi mini baiwar wani yaro daga gareka, wanda zai taimaka mini.**

**(6) Wanda zai gaji Annabta daga wuri na, da kuma wurin iyalan Annabi Yaqub (A.S), kuma ka sanya shi – Ya Ubangijina- ya zama yardajje cikin addininsa da halinsa da iliminsa.**

**(7) Sai Allah ya amsa masa addua'rsa, ya kira shi da cewa: "Ya kai Zakariyya, lallai muna maka albishir, mun amsa addu'arka, mun baka xa, sunansa Yahaya, bamu tava saka wa wani wannan sunan ba gabaninsa".**

**(8) Annabi Zakariyya ya ce, cikin mamakin ikon Allah,: "Yaya za a haifa mini da yaro, alhali mata ta bakararriya ce, bata haihuwa, kuma ni ga shi na kai qarshen rayuwa saboda girma da raunin qasusuwa?!".**

**(9) Sai Mala'ika ya ce: "Lamarin kamar yadda ka faxa ne, cewa matarka bata haihuwa, kuma ka kai matuqa cikin girma da raunin qasusuwa. Amma Ubangijinka ya ce: "Halitar Yahaya daga uwa bakararriya da uba wanda ya kai matuqar girma, abu ne mai sauki a wurin Ubangijinka, kuma ai tabbas ni na halicceka – kai Zakariyya - gabanin haka, alhali baka kasance wani abu da za a iya ambato ba, saboda ka kasance babu ne".**

**(10) Sai Annabi Zakariyya (A.S) ya ce: "Ya Ubangijina, ka sanya mini wata alamar da hankalina zai kwanta da ita, wadda zata nuna min tabbatuwar abin da Mala'iku suka yi mini albishir da shi". Sai ya ce: "Alamarka na samuwar abin da aka yi maka albishiri da shi, shi ne, ka kasa iya magana da mutane, tsawon dare uku, ba tare da wata rashin lafiya ba, kana cikin qoshin lafiyarka".**

**(11) Sai Annabi Zakariyya (A.S) ya fita daga wurin sallarsa zuwa wurin mutanensa, ya yi musu ishara ba tare da magana ba ce wa: "Ku yi tasbihi ga Allah mai tsarki safiya da marece".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Rauni da gajiyawa suna daga cikin mafi soyuwar hanyoyi na neman tsani zuwa ga Allah, domin suna nuna mutum ba shi da dabara da qarfi, kuma ya rataya zuciyarsa ga dabara da qarfin Allah.**

**2 - An so ga mutum ya ambaci ni'imomin da Allah da ya yi masa, da duk wani abin da yake nuna qanqan-da-kai a cikin addu'arsa.**

**3 - Kulawa da maslahar addini da kuma fifita ta a kan sauran maslaha.**

**4 - An so a saka wa yara sunaye masu kyawawan ma'anoni.**

يَٰيَحْيَىٰ خُذِ ٱلْكِتَٰبَ بِقُوَّةٍ ۖ وَءَاتَيْنَٰهُ ٱلْحُكْمَ صَبِيًّا ١٢
وَحَنَانًا مِّن لَّدُنَّا وَزَكَوٰةً ۖ وَكَانَ تَقِيًّا ١٣ وَبَرًّۢا بِوَٰلِدَيْهِ وَلَمْ
يَكُن جَبَّارًا عَصِيًّا ١٤ وَسَلَٰمٌ عَلَيْهِ يَوْمَ وُلِدَ وَيَوْمَ يَمُوتُ
وَيَوْمَ يُبْعَثُ حَيًّا ١٥ وَٱذْكُرْ فِى ٱلْكِتَٰبِ مَرْيَمَ إِذِ ٱنتَبَذَتْ
مِنْ أَهْلِهَا مَكَانًا شَرْقِيًّا ١٦ فَٱتَّخَذَتْ مِن دُونِهِمْ حِجَابًا
فَأَرْسَلْنَآ إِلَيْهَا رُوحَنَا فَتَمَثَّلَ لَهَا بَشَرًا سَوِيًّا ١٧ قَالَتْ إِنِّىٓ
أَعُوذُ بِٱلرَّحْمَٰنِ مِنكَ إِن كُنتَ تَقِيًّا ١٨ قَالَ إِنَّمَآ أَنَا۠ رَسُولُ
رَبِّكِ لِأَهَبَ لَكِ غُلَٰمًا زَكِيًّا ١٩ قَالَتْ أَنَّىٰ يَكُونُ لِى
غُلَٰمٌ وَلَمْ يَمْسَسْنِى بَشَرٌ وَلَمْ أَكُ بَغِيًّا ٢٠ قَالَ كَذَٰلِكِ
قَالَ رَبُّكِ هُوَ عَلَىَّ هَيِّنٌ ۖ وَلِنَجْعَلَهُۥٓ ءَايَةً لِّلنَّاسِ وَرَحْمَةً
مِّنَّا ۚ وَكَانَ أَمْرًا مَّقْضِيًّا ٢١ ۞ فَحَمَلَتْهُ فَٱنتَبَذَتْ بِهِۦ نصف الحزب ٣١
مَكَانًا قَصِيًّا ٢٢ فَأَجَآءَهَا ٱلْمَخَاضُ إِلَىٰ جِذْعِ ٱلنَّخْلَةِ
قَالَتْ يَٰلَيْتَنِى مِتُّ قَبْلَ هَٰذَا وَكُنتُ نَسْيًا مَّنسِيًّا ٢٣
فَنَادَىٰهَا مِن تَحْتِهَآ أَلَّا تَحْزَنِى قَدْ جَعَلَ رَبُّكِ تَحْتَكِ سَرِيًّا ٢٤
وَهُزِّىٓ إِلَيْكِ بِجِذْعِ ٱلنَّخْلَةِ تُسَٰقِطْ عَلَيْكِ رُطَبًا جَنِيًّا ٢٥



**(12) Sai aka haifar masa da Yahaya. Yayin da ya kai shekarar da za a iya yi masa magana sai muka ce masa: "Ya kai Yahaya, Ka riqi Attaura da qarfi da qoqari, kuma mun bashi fahimta da ilimi da qoqari da jajircewa tun yana shekarun yarinta".**

**(13) Kuma mun yi masa wata rahama daga wurinmu, mun tsarkake shi daga zunubi, kuma ya kasance mai tsoron Allah, yana bin umarnin Allah, yana nesantar abubuwan da ya hana.**

**(14) Ya kasance mai biyayya ga iyayensa, mai tausaya musu, mai kyautata musu. Bai kasance mai girman kai wajen biyayya ga Ubangijinsa da iyayensa ba, kuma bai kasance mai sava wa Allah da iyayensa ba.**

**(15) Aminci daga Allah ya tabbata a gare shi, ranar da aka haife shi, da ranar da zai mutu, ya fita daga wannan rayuwar, da ranar da za a tayar da shi da rai a ranar alqiyama. Waxannan wurare guda uku sune mafi wahalar wuraren da mutum yake wucewa ta kansu, don haka idan ya aminta a cikinsu, to babu tsoro a kansa dangane sauran wurare.**

**(16) Kuma ka ambaci labarin Nana Maryam (A.S) – Ya kai wannan Manzo - a cikin Alqur'anin da aka saukar maka, yayin da ta nesanci iyalinta, ta kaxaita a wani wuri can gabas da su.**

**(17) Sai ta sanya shamaki tsakaninta da mutanenta, saboda kar su ganta a lokacin da take ibada ga Ubangijinta, sai muka aiko mata da Mala'ika Jibrilu (A.S), ya fito mata da kamannin mutum mai cikakken halitta, sai ta ji tsoron kar dai yana nemanta da wani mummunan abu ne.**

**(18) Yayin da ta gan shi a kamannin cikakken mutum, yana fuskantar wurinta sai ta ce: "Ina neman tsarin Allah mai rahama daga gareka, kar ka yi min wani mummunan abu – Ya kai wannan mutum - in har ka kasance kana tsoron Allah". (19) Sai Mala'ika jibrilu (A.S) ya ce: "Ni ba mutum bane, ki Sani ni xan aike ne daga Ubangijinki zuwa gare ki, domin in yi ba ki xa nagartacce, mai tsarki".**

**(20) Sai Nana Maryam ta ce, tana cike da mamaki: "Ta yaya zan samu xa, alhali babu mutum miji ko waninsa da ya tava kusanta ta, kuma ni ba mazinaciya ba ce, ballantana in haifi xan zina?!"**

**(21) Sai Mala'ika Jibrilu (A.S) ya ce ma ta: "Lamarin haka yake, kamar yadda kika faxa, cewa xa namiji bai tava kusantarki ba, kuma ke ba mazinaciya ba ce. Amma dai Ubangijinki ya ce: "Halittar xa ba tare da uba ba, abu ne mai sauki a wurina, kuma saboda xan da za a baki ya zama alama ga mutane bisa ikon Allah, kuma wata rahama ce ta musamman daga wurinmu zuwa gare ki, da duk wanda ya yi imani da shi. Kuma halittar wannan yaron na ki qaddara ce daga wurin Allah abar zartarwa, rubutacce a cikin lauhul mahfuz.**

**(22) Sai ta xauki cikinsa, bayan Mala'ika ya yi mata busa, ta nesanci mutanenta da cikin, zuwa wani wuri mai nisa, inda babu mutane. (23) Sai naquda ta kama ta, ta tsugunnar da ita a wani reshen bishiyar dabino. Sai Nana Maryam (A.S) ta ce: "Kaicona! Ina ma dai na mutu kafin wannan rana, na kasance wani abun da ba a tuna da shi ba, saboda kar a yi mini mummunan zato". (24) Sai Annabi Isa (A.S) ya kira ta daga qarqashin qafafuwanta ya ce ma ta: "Kar ki yi baqin ciki. Allah ya sa ka miki wani idon ruwa wanda zaki sha daga cikinsa".**

**(25) Kuma ki kama kututturen dabinon nan, ki jijjiga shi, nunannun 'ya'yan dabino, sababbin tsinkewa za su faxo miki.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Yin haquri wajen tsayar da dokokin Shari'ah abu ne da ake buqatarsa.**

**2 - Xaukakar matsayin biyayya ga iyaye a wurin Allah. Don Allah ya haxa biyayyarsu da godiya a gare shi.**

**3 - Duk da cikar ikon Allah, wanda ya bayyanar da shi ga Nana Maryam, amma sai da ya umarce ta, ta yi riqo da sababi kafin 'ya'yan dabino su iso gare ta.**

فَكُلِي وَٱشۡرَبِي وَقَرِّي عَيۡنٗاۖ فَإِمَّا تَرَيِنَّ مِنَ ٱلۡبَشَرِ أَحَدٗا فَقُولِيٓ
إِنِّي نَذَرۡتُ لِلرَّحۡمَٰنِ صَوۡمٗا فَلَنۡ أُكَلِّمَ ٱلۡيَوۡمَ إِنسِيّٗا ٢٦ فَأَتَتۡ
بِهِۦ قَوۡمَهَا تَحۡمِلُهُۥۖ قَالُواْ يَٰمَرۡيَمُ لَقَدۡ جِئۡتِ شَيۡـٔٗا فَرِيّٗا ٢٧
يَٰٓأُخۡتَ هَٰرُونَ مَا كَانَ أَبُوكِ ٱمۡرَأَ سَوۡءٖ وَمَا كَانَتۡ
أُمُّكِ بَغِيّٗا ٢٨ فَأَشَارَتۡ إِلَيۡهِۖ قَالُواْ كَيۡفَ نُكَلِّمُ مَن كَانَ فِي
ٱلۡمَهۡدِ صَبِيّٗا ٢٩ قَالَ إِنِّي عَبۡدُ ٱللَّهِ ءَاتَىٰنِيَ ٱلۡكِتَٰبَ وَجَعَلَنِي
نَبِيّٗا ٣٠ وَجَعَلَنِي مُبَارَكًا أَيۡنَ مَا كُنتُ وَأَوۡصَٰنِي بِٱلصَّلَوٰةِ
وَٱلزَّكَوٰةِ مَا دُمۡتُ حَيّٗا ٣١ وَبَرَّۢا بِوَٰلِدَتِي وَلَمۡ يَجۡعَلۡنِي
جَبَّارٗا شَقِيّٗا ٣٢ وَٱلسَّلَٰمُ عَلَيَّ يَوۡمَ وُلِدتُّ وَيَوۡمَ أَمُوتُ
وَيَوۡمَ أُبۡعَثُ حَيّٗا ٣٣ ذَٰلِكَ عِيسَى ٱبۡنُ مَرۡيَمَۖ قَوۡلَ ٱلۡحَقِّ
ٱلَّذِي فِيهِ يَمۡتَرُونَ ٣٤ مَا كَانَ لِلَّهِ أَن يَتَّخِذَ مِن وَلَدٖۖ سُبۡحَٰنَهُۥٓۚ
إِذَا قَضَىٰٓ أَمۡرٗا فَإِنَّمَا يَقُولُ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ٣٥ وَإِنَّ ٱللَّهَ رَبِّي وَرَبُّكُمۡ
فَٱعۡبُدُوهُۚ هَٰذَا صِرَٰطٞ مُّسۡتَقِيمٞ ٣٦ فَٱخۡتَلَفَ ٱلۡأَحۡزَابُ مِنۢ
بَيۡنِهِمۡۖ فَوَيۡلٞ لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن مَّشۡهَدِ يَوۡمٍ عَظِيمٍ ٣٧ أَسۡمِعۡ بِهِمۡ
وَأَبۡصِرۡ يَوۡمَ يَأۡتُونَنَا لَٰكِنِ ٱلظَّٰلِمُونَ ٱلۡيَوۡمَ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ٣٨



**(26) Ki ci 'ya'yan dabinon, kuma ki sha ruwan qoramar, sannan ki yi farin ciki da jaririnki, kar ki yi baqin ciki. In kuma kin ga wani mutum ya tambaye ki labarin jaririn, to ki ce masa: “Haqiqa na xora wa kaina cewa zan yi shiru, saboda neman yardar Ubangijinka mai rahama, don haka yau ba zan yi magana da wani mutum ba”.**
**(27) Sai Nana Maryam ta zo da xanta wurin mutanenta, tana riqe da shi. Mutanenta cikin kyamata suka ce ma ta: “Ya ke Maryam, lallai kin zo da wani abu, wanda muninsa ya girmama, kin zo da yaro ba tare da uba ba!”.**
**(28) Ya ke wadda kika yi kama da Haruna a wajen ibada (wani mutumin kirki ne), babanki fa ba mazinaci ba ne, haka ma mahaifiyarki ba mazinaciya ba ce, ke daga tsarkakakken gida wanda aka san su da nagarta kike, don me zaki zo mana da yaro maras uba?!”.**
**(29) Sai ta yi nuni zuwa ga xan ta Annabi Isa (A.S) yana kan shimfixar haihuwa. Sai mutanenta cikin mamaki, suka ce ma ta: “Yaya zamu yi magana da jariri wanda yake kan shimfixar haihuwa?”**
**(30) Sai Annabi Isa (A.S) ya ce: “Lallai ni bawan Allah ne. Ya ba ni Injila kuma ya saka ni in zama xaya daga cikin Annabawansa”.**
**(31) “Kuma ya sanya ni mai yawan amfani ga bayinsa a duk inda na ke, kuma ya umarce ni da yin sallah, da bayar da zakka tsawon rayuwa ta”.**
**(32) “Kuma ya sanya ni mai biyayya ga mahaifiyata, bai mayar da ni mai girman kai, ko savo ba wajen biyayyar Ubangiji”.**
**(33) “Aminci daga sharrin shaixan da mataimakansa ya tabbata a kaina, ranar haihuwa ta, da ranar mutuwa ta, da ranar da za a tayar da ni da rai a gidan alqiyama. Don haka shaixan ba zai iya fizgata a waxannan matakai guda uku, masu ban tsoro ba”. (34) Wanda aka siffanta da waxancan siffofin shi ne Annabi Isa xan Nana Maryam (A.S). Kuma wannan maganan ita ce zancen gaskiya dangane da shi, ba abin da vatattu masu shakku dangane da shi suke faxa kuma suke savawa juna a ciki ba.**
**(35) Sam sam bai cancanta ga Allah ba ya xauki wani a matsayin xa. Ya xaukaka, ya tsarkaka daga yin haka. Duk lokacin da ya yi nufin wani abu, to kawai yana ce wa abin ne “kasance”, sai ya kasance. Duk wanda ya kasance haka to ya fi qarfin a jingina masa xa. (36) Haqiqa Allah mai tsarki shi ne Ubangijina kuma shi ne Ubangijinku gaba xaya. Don haka ku yi ikhlasi a gare shi, ku kaxaita shi da bauta, shi kaxai. Wannan abin da na faxa muku shi ne tafarki madaidaici, mai isarwa zuwa ga yardar Allah. (37) Amma sai masu savani cikin mutanensa suka yi savani dangane da lamarin Annabi Isa (A.S), suka zama qungiyoyi daban daban. Wasun su suka yi imani da shi, suka ce: “shi Manzo ne”. Wasu suka kafirce masa kamar Yahudawa. Wasu vangarorin kuma suka wuce gona da iri, suka ce: “shi ne Allah”. Wasu kuma suka ce: “shi xan Allah ne”. Allah ya xaukaka daga dukkanin waxannan zantuka. azaba ta tabbata ga masu savani a cikinsa ranar da za su shaidi tashin alqiyama da abin da ke cikinta na hisabi da uquba. (38) Waye zai fi su ji da gani a wannan ranar, za su ji a lokacin da ji ba zai amfane su ba. Za su gani a lokacin da gani ba zai amfane su ba. Amma dai azzalumai sun cikin vata bayyananne daga tafarki madaidaici a rayuwar duniya, don haka ba sa yin shiri don lahira, har sai ta zo musu kwatsam, suna kan zaluncinsu.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Yin umarni ga Nana Maryam (A.S) cewa ta yi shiru yana nuna falalar shiru a wasu wuraren.**
**2 - Ba ya halatta a yi bakancen yin shiru a shari'armu. 3 - Abin da Alqur'ani ya ba da labarinsa na halittar Annabi Isa (A.S) shi ne yankakken gaskiyar da babu shakka a cikinta. Kuma duk wani abin da ya sava masa na zance to qarya ne, bai dace da Manzanni ba. 4 - Kafiri yana zama kurma makaho daga gaskiya a duniya, amma zai ji kuma zai gani a lahira, idan ya ga azaba, sai dai hakan (ji da ganin gaskiyar) ba zai tava amfanar shi ba.**

وَأَنذِرۡهُمۡ يَوۡمَ ٱلۡحَسۡرَةِ إِذۡ قُضِيَ ٱلۡأَمۡرُ وَهُمۡ فِي غَفۡلَةٖ وَهُمۡ لَا يُؤۡمِنُونَ
٣٩ إِنَّا نَحۡنُ نَرِثُ ٱلۡأَرۡضَ وَمَنۡ عَلَيۡهَا وَإِلَيۡنَا يُرۡجَعُونَ ٤٠ وَٱذۡكُرۡ
فِي ٱلۡكِتَٰبِ إِبۡرَٰهِيمَۚ إِنَّهُۥ كَانَ صِدِّيقٗا نَّبِيًّا ٤١ إِذۡ قَالَ لِأَبِيهِ يَٰٓأَبَتِ
لِمَ تَعۡبُدُ مَا لَا يَسۡمَعُ وَلَا يُبۡصِرُ وَلَا يُغۡنِي عَنكَ شَيۡـٔٗا ٤٢ يَٰٓأَبَتِ
إِنِّي قَدۡ جَآءَنِي مِنَ ٱلۡعِلۡمِ مَا لَمۡ يَأۡتِكَ فَٱتَّبِعۡنِيٓ أَهۡدِكَ صِرَٰطٗا
سَوِيّٗا ٤٣ يَٰٓأَبَتِ لَا تَعۡبُدِ ٱلشَّيۡطَٰنَۖ إِنَّ ٱلشَّيۡطَٰنَ كَانَ لِلرَّحۡمَٰنِ
عَصِيّٗا ٤٤ يَٰٓأَبَتِ إِنِّيٓ أَخَافُ أَن يَمَسَّكَ عَذَابٞ مِّنَ ٱلرَّحۡمَٰنِ
فَتَكُونَ لِلشَّيۡطَٰنِ وَلِيّٗا ٤٥ قَالَ أَرَاغِبٌ أَنتَ عَنۡ ءَالِهَتِي
يَٰٓإِبۡرَٰهِيمُۖ لَئِن لَّمۡ تَنتَهِ لَأَرۡجُمَنَّكَۖ وَٱهۡجُرۡنِي مَلِيّٗا ٤٦ قَالَ
سَلَٰمٌ عَلَيۡكَۖ سَأَسۡتَغۡفِرُ لَكَ رَبِّيٓۖ إِنَّهُۥ كَانَ بِي حَفِيّٗا ٤٧
وَأَعۡتَزِلُكُمۡ وَمَا تَدۡعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَأَدۡعُواْ رَبِّي عَسَىٰٓ أَلَّآ
أَكُونَ بِدُعَآءِ رَبِّي شَقِيّٗا ٤٨ فَلَمَّا ٱعۡتَزَلَهُمۡ وَمَا يَعۡبُدُونَ مِن
دُونِ ٱللَّهِ وَهَبۡنَا لَهُۥٓ إِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَۖ وَكُلّٗا جَعَلۡنَا نَبِيّٗا ٤٩
وَوَهَبۡنَا لَهُم مِّن رَّحۡمَتِنَا وَجَعَلۡنَا لَهُمۡ لِسَانَ صِدۡقٍ عَلِيّٗا ٥٠
وَٱذۡكُرۡ فِي ٱلۡكِتَٰبِ مُوسَىٰٓۚ إِنَّهُۥ كَانَ مُخۡلَصٗا وَكَانَ رَسُولٗا نَّبِيّٗا ٥١



**39 Ka yi wa mutane gargaxi –Ya kai wannan
Manzo- dangane da ranar nadama, yayin da
wanda ya munana aiki zai yi nadama akan
mummunan aikinsa. Haka nan wanda ya kyautata
aiki shi ma zai yi nadamar rashin yawaita ayyukan
biyayyarsa, bayan an riga an naxe takardun
rubuta aikin bayi, an gama musu hisabi, kowa
ya isa zuwa ga abin da ya gabatar, irin wanda
suka kasance suna ruxuwa da shi a rayuwar su ta
duniya, suna cikin rafkanuwa dangane da lahira,
basu yi imani da ranar alqiyama ba. 40 Mu ne
masu wanzuwa bayan gushewar halittu, zamu gaji
qasa da wanda suke a bayanta, saboda gushewarsu
da wanzuwarmu, da mallakarmu a gare su, da
saraffa su da muke yi yadda muke so, kuma zuwa
garemu ne kaxai za a mayar dasu a ranar alqiyama
don hisabi da sakamako. 41 Ka ambaci labarin
Annabi Ibrahim (A.S) – Ya kai wannan Manzo-
a cikin Alqur'ani da aka saukar maka, haqiqa ya
kasance mai yawan gaskiya da gaskata ayoyin
Allah, kuma Annabi daga wurin Allah.
42 Yayin da ya ce wa babansa Azara: "Ya baba
na, don me kake bauta wa gunkin da baya jin
kiranka idan ka kira shi, baya ganin bautarka
idan ka bauta masa, kuma ba zai iya yaye maka
wata cuta, ko ya jawo maka wani amfani ba?!".
43 "Ya baba na, haqiqa wani ilimi ya zo min ta
hanyar wahayi, ilimin da bai zo maka ba, don haka
ka bi ni, in shiryar da kai tafarki madaidaici".
44 "Ya baba na, kar ka bauta wa shaixan ta hanyar
biyayya a gare shi. Lallai shaixan ya kasance mai
savo ne ga Ubangijinsa, tun daga lokacin da ya
umurce shi ya yi sujjada ga Annabi Adam (A.S) amma ya qi ya yi sujjadar". 45 "Ya baba na, lallai ina jin tsoron
wata azaba daga Allah mai rahama ta shafe ka, in har ka mutu akan kafircinka, sai ka zama abokin shaixan cikin
azaba, sobada biyayyarka a gare shi". 46 Sai Azara ya ce wa xansa Annabi Ibrahim (A.S): "Yanzu ka juya baya
ga gumakan da nake bauta musu, ya kai Ibrahim?! Wallahi idan baka daina sukan gumaka na ba, zan cefe ka da
duwatsu, kuma ka rabu da ni lokaci mai tsawo, kar ka qara zuwa inda nake". 47 Sai Annabi Ibrahim (A.S) ya ce wa
babansa: "Aminci ya tabbata a kanka daga gare ni. Ba zan yi maka abin da baka so ba. Zan nema maka gafara da
shiriya daga Ubangijina. Lallai Ubangijina mai yawan tausaya mini ne". 48 "Kuma zan rabu daku da abubuwan
bautarku, waxanda kuke bautata musu koma bayan Allah. Zan bauta wa Ubangijina shi kaxai, ban zan haxa wani
da shi ba, ina fatan ba zai hana ni abin da na nema ba, idan na kira shi, don kada in zama marashin arziki da
kiransa". 49 Yayin da ya rabu da su da abubuwan da suke bautawa, waxanda suke bautawa koma bayan Allah, sai
muka maye masa gurbin rashin iyali da ba shi kyautar xa, shi ne Annabi Is'haqa (A.S) da jika Annabi Yaqub (A.S),
kowannensu mun sanya shi Annabi. 50 Muka ba su daga rahamar mu alheri mai yawa, tare da Annabci, kuma
muka sanya musu kyakkyawan yabo mai xorewa a harshen bayi. 51 Ka ambaci labarin Annabi Musa (A.S) – Ya
kai wannan Manzo- a cikin Alqur'anin da aka saukar maka, lallai shi ya kasance zavavve ne, Manzo kuma Annabi.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Da yake qauracewar Annabi Ibrahim da ya yi wa mutanensa, suna tare ne da matarsa Saratu ne, don haka sai ya dace a ambaci kyautar da aka yi musu, wadda suka yi tarayya a cikinta, kyautar xa da jika, sannan sai aka ambaci Annabi Isma'il shi kaxai daga baya, duk da cewa Allah ya yi masa kyautarsa tun kafin Annabi Is'haq.**

**2 - Koya mana ladabi da tausasawa da rangwane wajen tattaunawa da iyaye da zavar mafi kyan suna don kiransu da shi. 3 - Savo yana hana bawa samun rahamar Allah, yana rufe masa qofofinta, kama yadda xa'a kuma a gefe guda ita ce mafi girman hanya na samu rahamar Allah. 4 - Allah ya yi alqawari ga duk mai kyautata aiki cewa zai yaxa kyakkyawan ambatonsa da yabo cikin mutane, gwargwadon kyautatawarsa, kuma Annabi Ibrahim (A.S) da zuriyarsa suna cikin shugabannin masu kyautatawa.**

وَنَٰدَيۡنَٰهُ مِن جَانِبِ ٱلطُّورِ ٱلۡأَيۡمَنِ وَقَرَّبۡنَٰهُ نَجِيّٗا ٥٢ وَوَهَبۡنَا لَهُۥ مِن
رَّحۡمَتِنَآ أَخَاهُ هَٰرُونَ نَبِيّٗا ٥٣ وَٱذۡكُرۡ فِي ٱلۡكِتَٰبِ إِسۡمَٰعِيلَۚ إِنَّهُۥ كَانَ
صَادِقَ ٱلۡوَعۡدِ وَكَانَ رَسُولٗا نَّبِيّٗا ٥٤ وَكَانَ يَأۡمُرُ أَهۡلَهُۥ بِٱلصَّلَوٰةِ
وَٱلزَّكَوٰةِ وَكَانَ عِندَ رَبِّهِۦ مَرۡضِيّٗا ٥٥ وَٱذۡكُرۡ فِي ٱلۡكِتَٰبِ إِدۡرِيسَۚ إِنَّهُۥ
كَانَ صِدِّيقٗا نَّبِيّٗا ٥٦ وَرَفَعۡنَٰهُ مَكَانًا عَلِيًّا ٥٧ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ أَنۡعَمَ
ٱللَّهُ عَلَيۡهِم مِّنَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ مِن ذُرِّيَّةِ ءَادَمَ وَمِمَّنۡ حَمَلۡنَا مَعَ نُوحٖ وَمِن
ذُرِّيَّةِ إِبۡرَٰهِيمَ وَإِسۡرَٰٓءِيلَ وَمِمَّنۡ هَدَيۡنَا وَٱجۡتَبَيۡنَآۚ إِذَا تُتۡلَىٰ عَلَيۡهِمۡ
سَجدَة ءَايَٰتُ ٱلرَّحۡمَٰنِ خَرُّواْۤ سُجَّدٗاۤ وَبُكِيّٗا ۩ ٥٨ ۞ فَخَلَفَ مِنۢ بَعۡدِهِمۡ
خَلۡفٌ أَضَاعُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَٱتَّبَعُواْ ٱلشَّهَوَٰتِۖ فَسَوۡفَ يَلۡقَوۡنَ غَيًّا
٥٩ إِلَّا مَن تَابَ وَءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحٗا فَأُوْلَٰٓئِكَ يَدۡخُلُونَ ٱلۡجَنَّةَ
وَلَا يُظۡلَمُونَ شَيۡـٔٗا ٦٠ جَنَّٰتِ عَدۡنٍ ٱلَّتِي وَعَدَ ٱلرَّحۡمَٰنُ عِبَادَهُۥ
بِٱلۡغَيۡبِۚ إِنَّهُۥ كَانَ وَعۡدُهُۥ مَأۡتِيّٗا ٦١ لَّا يَسۡمَعُونَ فِيهَا لَغۡوًا إِلَّا
سَلَٰمٗاۖ وَلَهُمۡ رِزۡقُهُمۡ فِيهَا بُكۡرَةٗ وَعَشِيّٗا ٦٢ تِلۡكَ ٱلۡجَنَّةُ ٱلَّتِي
نُورِثُ مِنۡ عِبَادِنَا مَن كَانَ تَقِيّٗا ٦٣ وَمَا نَتَنَزَّلُ إِلَّا بِأَمۡرِ رَبِّكَۖ لَهُۥ
مَا بَيۡنَ أَيۡدِينَا وَمَا خَلۡفَنَا وَمَا بَيۡنَ ذَٰلِكَۚ وَمَا كَانَ رَبُّكَ نَسِيّٗا ٦٤



**(52) Mun kira shi daga gefen dutsen ta damarsa, duba da inda Annabi Musa yake a tsaye, Mun kusanto da shi don ganawa, ta inda Allah ya jiyar da shi maganarsa.**
**(53) Muka ba shi – daga cikin rahamarmu da ni'imarmu - xan 'uwansa Haruna (A.S) ya zama Annabi, don amsa addu'arsa yayin da ya roqi hakan a wurin Ubangijinsa.**
**(54) Ka ambaci labarin Annabi Isma'ila (A.S) – Ya kai wannan Manzo- a cikin Alqur'anin da aka saukar maka, haqiqa ya kasance mai cika alqawari ne, baya yin alqawari face sai ya cika shi, kuma ya kasance Manzo ne Annabi.**
**(55) Ya kasance yan umurtar iyalansa da tsayar da salla, da bayar da zakka. Kuma ya kasance yardajje ne a wurin Ubangijinsa.**
**(56) Ka ambaci labarin Annabi Idris (A.S) – Ya kai wannan Manzo - a cikin Alqur'anin da aka saukar maka, haqiqa ya kasance mai yawan gaskiya ne da gasgata ayoyin Ubangijinsa, kuma Annabi ne daga cikin Annabawan Allah.**
**(57) Kuma mun xaukaka ambatonsa da abin da muka ba shi na Annabci, don haka ya kasance mai babban matsayi.**
**(58) Waxannan da aka ambace su a wannan Surar, tun daga Annabi Zakariyya har zuwa Annabi Idris (A.S), su ne waxanda Allah ya yi musu ni'ima ta Annabci, cikin 'ya'yan Annabi Adam (A.S) da 'ya'yan mutanen da muka xauke su a cikin jirgin ruwa tare da Annabi Nuhu (A.S) da 'ya'yan Annabi Ibrahim da Annabi Yaqub (A.S) da waxanda muka yi musu dacen riqo da Musulunci, muka zave su, muka sanya su Annabawa. Sun kasance idan sun ji ana karanta ayoyin Allah, sai su faxi qasa su yi sujjada, suna kuka saboda tsoron Allah. (59) Bayan waxannan Annabawa sun wuce, sai wasu munanan mabiya vatattu suka biyo bayansu, suka tozarta sallah, ba su yi ta ba akan yadda ake so, suka aikata abin da zuciyarsu take so, na savo, kamar zina, don haka da sannu zasu gamu da sharri da tavewa a cikin Jahannama.**
**(60) Sai dai wanda ya tuba daga gazawarsa da sakacinsa, yayi imani da Allah, ya aikata ayyuka nagari, to waxanda suka siffantu da waxannan siffofin za su shiga Aljanna, kuma ba za a tauye musu komai daga cikin ladan ayyukansu ba, komai qanqantarsa. (61) Aljannatai ne na zama da tabbatuwa a ciki, wanda Allah mai rahama ya yi wa bayinsa nagartattu alqawari za su shiga cikinsu, alhali ba su gan su da idanuwansu ba, amma sai suka bayar da gaskiya da su. Haqiqa alqawarin Allah – duk da ba a ganin sa - mai zuwa ne babu makawa a kan haka.**
**(62) Basa jin maganganu marasa amfani da maganganun banza a cikin su, sai dai su ji gaisuwar aminci, sashensu ga sashe, da gaisuwar aminci daga Mala'iku, duk abin da suke sha'awa na abinci ana kawo musu shi, safiya da maraice.**
**(63) Wannan Aljannar da aka siffanta ta da waxannan siffofin, ita ce zamu gadar da ita ga bayinmu waxanda suka kasance masu aiwatar da umarnin mu, da nisantar abubuwan da muka hana. Yayin da Allah Maxaukin Sarki ya ambaci siffofin masu tsoron Allah, sai ya ambaci cewa tsoron Allah shi ne tsayuwa a kan umarnisa, ya ce:**
**(64) Ka gaya wa Annabi Muhammad (S.A.W) - Ya kai Jibrilu cewa: "Lallai Mala'iku ba sa saukowa haka kawai a karan kansu, suna saukowa ne kaxai da umarnin Allah. Kuma abin da muke fuskanta a gaba na lamarin lahira, na Allah ne, haka ma abin da zamu bari a baya na lamarin duniya, shima na Allah ne, haka ma abin da yake tsakanin duniya da lahira. Kuma Ubangijinka – Ya kai wannan Manzo - bai kasance mai mantuwa ba.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Buqatuwar mai kira zuwa ga Allah a kowane lokaci zuwa ga masu taimako, waxanda za su taimaka masa wajen yaxa da'awarsa. 2 - Tabbatar da siffar magana ga Allah Maxaukakin Sarki. 3 - Cika alqawari abin yabo ne, kuma yana daga cikin xabi'ar Annabawa da Manzanni. Kishiyar hakan shi ne sava alqawari, shi kuma abin zargi ne. 4 - Mala'iku 'yan saqon Allah ne da wahayi, basa sauka zuwa wurin wani Annabi ko Manzo daga cikin mutane sai da umarnin Allah.**

رَّبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَيۡنَهُمَا فَٱعۡبُدۡهُ وَٱصۡطَبِرۡ لِعِبَٰدَتِهِۦۚ
هَلۡ تَعۡلَمُ لَهُۥ سَمِيّٗا ٦٥ وَيَقُولُ ٱلۡإِنسَٰنُ أَءِذَا مَا مِتُّ لَسَوۡفَ
أُخۡرَجُ حَيًّا ٦٦ أَوَلَا يَذۡكُرُ ٱلۡإِنسَٰنُ أَنَّا خَلَقۡنَٰهُ مِن قَبۡلُ
وَلَمۡ يَكُ شَيۡـٔٗا ٦٧ فَوَرَبِّكَ لَنَحۡشُرَنَّهُمۡ وَٱلشَّيَٰطِينَ ثُمَّ
لَنُحۡضِرَنَّهُمۡ حَوۡلَ جَهَنَّمَ جِثِيّٗا ٦٨ ثُمَّ لَنَنزِعَنَّ مِن كُلِّ
شِيعَةٍ أَيُّهُمۡ أَشَدُّ عَلَى ٱلرَّحۡمَٰنِ عِتِيّٗا ٦٩ ثُمَّ لَنَحۡنُ أَعۡلَمُ بِٱلَّذِينَ
هُمۡ أَوۡلَىٰ بِهَا صِلِيّٗا ٧٠ وَإِن مِّنكُمۡ إِلَّا وَارِدُهَاۚ كَانَ عَلَىٰ رَبِّكَ
حَتۡمٗا مَّقۡضِيّٗا ٧١ ثُمَّ نُنَجِّي ٱلَّذِينَ ٱتَّقَواْ وَّنَذَرُ ٱلظَّٰلِمِينَ
فِيهَا جِثِيّٗا ٧٢ وَإِذَا تُتۡلَىٰ عَلَيۡهِمۡ ءَايَٰتُنَا بَيِّنَٰتٖ قَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ
لِلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَيُّ ٱلۡفَرِيقَيۡنِ خَيۡرٞ مَّقَامٗا وَأَحۡسَنُ نَدِيّٗا ٧٣
وَكَمۡ أَهۡلَكۡنَا قَبۡلَهُم مِّن قَرۡنٍ هُمۡ أَحۡسَنُ أَثَٰثٗا وَرِءۡيٗا ٧٤
قُلۡ مَن كَانَ فِي ٱلضَّلَٰلَةِ فَلۡيَمۡدُدۡ لَهُ ٱلرَّحۡمَٰنُ مَدًّاۚ حَتَّىٰٓ إِذَا رَأَوۡاْ
مَا يُوعَدُونَ إِمَّا ٱلۡعَذَابَ وَإِمَّا ٱلسَّاعَةَ فَسَيَعۡلَمُونَ مَنۡ هُوَ شَرّٞ
مَّكَانٗا وَأَضۡعَفُ جُندٗا ٧٥ وَيَزِيدُ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ٱهۡتَدَوۡاْ هُدٗىۗ
وَٱلۡبَٰقِيَٰتُ ٱلصَّٰلِحَٰتُ خَيۡرٌ عِندَ رَبِّكَ ثَوَابٗا وَخَيۡرٞ مَّرَدًّا ٧٦



**65 Mahaliccin Sammai da Qassai, Mamallakinsu, mai gudanar da lamarinsu. Mahaliccin abin da yake tsakaninsu, Mamallakinsu, mai gudanar da lamarinsu, Don haka ka bauta masa shi kaxai, saboda shi ne wanda ya cancanci a yi masa bauta. Kuma ka tabbata akan bautarsa, ba shi da wani makamanci ko kini wanda yake tarayya da shi wajen cancantar bauta. 66 Kafiri mai inkarin tashi bayan mutuwa yana cewa cikin izgilanci: "Ashe idan na mutu za a sake fitar da ni daga qabari na a raye, wata rayuwar ta biyu?! Kai wannan magana ta yi nisa da hankali. 67 Shin wannan mai inkarin tashi bayan mutuwa, baya tuna cewa mu muka halicce shi tun gabanin haka, alhali kafin lokacin shi ba komai ba ne?! To ya kafa hujja da halittar farkon akan yiwuwar halitta ta biyun, duk da cewa ma, halittar ta biyun ta fi sauqi. 68 To, na rantse da Ubangijinka – Ya kai wannan Manzo- lallai zamu fitar da su daga qaburburansu zuwa farfajiyar taron alqiyama, tare da shaixanunsu, waxanda suka vatar da su, sannan zamu kora su zuwa qofofin wutan Jahannama suna qasqantattu, suna durqushe akan gwiwoyinsu. 69 Sannan zamu fizgo - daga kowace al'umma cikin vatattun al'ummu- waxanda suka fi tsananin savo da girman kai wajen bin umarnin Allah mai rahama, wato shugabanninsu, (Mu fara jefa su a cikin wuta).**

**70 Sannan mu ne muka fi sanin waxanda suka fi cancanta su shiga wuta, su xanxani zafinta da wahalhalunta. 71 Babu wani daga cikinku – Ya ku mutane - face sai ya wuce ta kan siraxin da ya ke saman wutan Jahannama. Wannan wucewar qaddara ce tabbatacciyya da Allah ya qaddara, kuma ya zartar da ita, don haka babu mai mayar da qaddarar Allah. 72 Sannan sai mu kuvutar da waxanda suka ji tsoron Ubangijinsu ta hanyar biyayya ga umarninsa da nesantar haninsa, mu qyale azzalumai suna durqushe a kan gwiwowinsu, ba za su iya tsere mata, ko su kuvuta daga faxawa cikin wuta ba.**

**73 Duk lokacin da ake karanta wa mutane ayoyinmu bayyanannu, waxanda aka saukar wa Manzonmu, sai Kafirai su ce wa muminai: "Wane vangare ne ya fi kyawun matsayi da mazauni, da kyawun matattara da majalisa, cikin vangarorin nan biyu, na mu ko na ku?." 74 Al'ummu guda nawa ne muka halaka su gabanin waxannan kafirai, masu alfahari da abin da da suke da shi, na ci gaban rayuwa, waxanda suka fi waxannan kyawun dukiya da kyawun gani, saboda tsadan tufafinsu da jin dadi a jikinsu!".**

**75 Ka ce – Ya kai wannan Manzo -: "Duk wanda ya kasance yana faganniya cikin vatansa to da sannu Allah mai rahama zai yi mi shi talala, har ya qara dulmiya cikin vatansa, har in sun yi ido huxu da abin da ake musu narkonsa na azabar da za a gaggauta musu a duniya, ko wadda za a jinkirta ta zuwa ranar alqiyama, sannan za su san waye wanda ya fi munin matsayi da qarancin mataimaka, vangarensu ko vangaren Muminai?!".**

**76 Jinkirtawa waxancan don su qara vata, a gefe guda kuma Allah yana qarawa waxanda suka shiriya imani da biyayya ga Allah, da ayyuka nagartattu waxanda suke kaiwa zuwa ga arziki na har abada, kuma mafi amfani a wajen Ubangijinka – Ya kai wannan Manzo – sakamako ne da kyakkyawan qarshe.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Wajibi ne a kan muminai su shagaltu da abin da Allah ya umarce su da shi, su tabbata a kansa gwargwadon iyawarsu. 2 - Qetarewar halittu gaba xayansu ta kan wuta – wato wucewar su ta kan siraxi, ba shiga cikin wuta ba - abu ne wanda zai faru tabbas, babu makawa. 3 - Ma'aunin ingantacciyar fahimtar addini ya sha bamban da tunanin gama garin mutane da jahilai. 4 - Duk wanda ya nitse cikin vata, ya girku cikin kafirci, to Allah yakan qyale shi cikin shisshigin jahilci da kafircinsa, har ya qara dulmiya cikin ruxunsa, sai hakan ya zama sababin qarin tsananin uquba a gare shi. 5 - Allah yana tabbatar da muminai a kan shiriya, kuma yana qara musu dace da nasara, kuma yana saukar da ayoyi waxanda zasu zama sababin qara musu yaqini don sakayya a gare su.**

أَفَرَءَيْتَ ٱلَّذِى كَفَرَ بِـَٔايَـٰتِنَا وَقَالَ لَأُوتَيَنَّ مَالًا وَوَلَدًا
٧٧ أَطَّلَعَ ٱلْغَيْبَ أَمِ ٱتَّخَذَ عِندَ ٱلرَّحْمَـٰنِ عَهْدًا ٧٨ كَلَّا
سَنَكْتُبُ مَا يَقُولُ وَنَمُدُّ لَهُۥ مِنَ ٱلْعَذَابِ مَدًّا ٧٩ وَنَرِثُهُۥ
مَا يَقُولُ وَيَأْتِينَا فَرْدًا ٨٠ وَٱتَّخَذُوا۟ مِن دُونِ ٱللَّهِ ءَالِهَةً
لِّيَكُونُوا۟ لَهُمْ عِزًّا ٨١ كَلَّا ۚ سَيَكْفُرُونَ بِعِبَادَتِهِمْ وَيَكُونُونَ
عَلَيْهِمْ ضِدًّا ٨٢ أَلَمْ تَرَ أَنَّآ أَرْسَلْنَا ٱلشَّيَـٰطِينَ عَلَى ٱلْكَـٰفِرِينَ
تَؤُزُّهُمْ أَزًّا ٨٣ فَلَا تَعْجَلْ عَلَيْهِمْ ۖ إِنَّمَا نَعُدُّ لَهُمْ عَدًّا ٨٤
يَوْمَ نَحْشُرُ ٱلْمُتَّقِينَ إِلَى ٱلرَّحْمَـٰنِ وَفْدًا ٨٥ وَنَسُوقُ ٱلْمُجْرِمِينَ
إِلَىٰ جَهَنَّمَ وِرْدًا ٨٦ لَّا يَمْلِكُونَ ٱلشَّفَـٰعَةَ إِلَّا مَنِ ٱتَّخَذَ عِندَ
ٱلرَّحْمَـٰنِ عَهْدًا ٨٧ وَقَالُوا۟ ٱتَّخَذَ ٱلرَّحْمَـٰنُ وَلَدًا ٨٨ لَّقَدْ
جِئْتُمْ شَيْـًٔا إِدًّا ٨٩ تَكَادُ ٱلسَّمَـٰوَٰتُ يَتَفَطَّرْنَ مِنْهُ
وَتَنشَقُّ ٱلْأَرْضُ وَتَخِرُّ ٱلْجِبَالُ هَدًّا ٩٠ أَن دَعَوْا۟ لِلرَّحْمَـٰنِ وَلَدًا
٩١ وَمَا يَنۢبَغِى لِلرَّحْمَـٰنِ أَن يَتَّخِذَ وَلَدًا ٩٢ إِن كُلُّ مَن فِى
ٱلسَّمَـٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ إِلَّآ ءَاتِى ٱلرَّحْمَـٰنِ عَبْدًا ٩٣ لَّقَدْ أَحْصَىٰهُمْ
وَعَدَّهُمْ عَدًّا ٩٤ وَكُلُّهُمْ ءَاتِيهِ يَوْمَ ٱلْقِيَـٰمَةِ فَرْدًا ٩٥



**(77) Ya kai wannan Annabi baka da labarin wanda ya kafircewa hujjojinmu, ya yi inkarin alqawarinmu na narkon azaba, kuma ya ce –: “In na mutu kuma aka tayar da ni, to lallai za a ba ni dukiya da 'ya'ya masu yawa?!”**

**(78) Shin ya san gaibu ne, shi ya sa ya faxi abin da ya faxa ba tare da dalili ba?!. Ko ya xauki alqawari ne a wurin Ubangijinsa cewa lallai zai shigar da shi Aljanna, ya ba shi dukiya da 'ya'ya?!.**

**(79) Abin ba kamar yadda yake riyawa ba ne! Lallai zamu rubuta abin da yake faxa, da abin da yake aikatawa, kuma zamu qara masa azaba qari akan azabarsa, saboda abin da yake riyawa na qarya da shirme.**

**(80) Kuma zamu gaji abin da ya bari na dukiya da 'ya'ya bayan mun halaka shi, kuma zai taho zuwa gare mu ranar alqiyama yana shi qaxai, tilo, an savule masa duk abin da yake jin daxi da shi na dukiya da matsayi.**

**(81) Mushirikai sun xauki wasu abubuwan bauta koma bayan Allah, wai don su zamar musu mataimaka, waxanda zasu samu taimako da xaukaka a wurinsu.**

**(82) Abin ba kamar yadda suke riyawa ba ne! Ai waxannan abubuwan bautar da suke bautawa koma bayan Allah xin, zasu musanta abin da mushirikai suka yi musu a ranar lahira, kuma za su yi baran baran da su, zasu zamar musu abokan gaba.**

**(83) Ba ka sani ba ne – Ya kai wannan Manzo – cewa: Mun aika shaixanu, mun xora su akan kafira, don su ziga su, su ingiza su zuwa ga savo da kawar da mutane daga hanyar Allah, ingizawa mai qarfi?.**

**(84) Don haka kar ka yi gaggawa – Ya kai wannan Manzo- wajen neman Allah ya gaggauta halaka su. Muna lissafe da rayuwarsu, har lokacin da aka xiba musu don talala ya qare, sai mu yi musu uquba da abin da ya dace da su.**

**(85) Ka ambaci ranar alqiyama – Ya kai wannan Manzo -, ranar da zamu tara masu tsoron Ubangijinsu – ta hanyar biyayya ga umarninsa da nesantar haninsa - Mu kai su wurin Ubangijinsu cikin tawaga - tawaga, ana girmama su.**

**(86) Mu tasa qeyar kafirai zuwa wutar Jahannama suna cike da qishin ruwa.**

**(87) Waxannan kafirai basa iya ceton junansu, (domin ranan babu ceto) sai fa ga wanda ya xauki alqawari a wurin Allah mai rahama na imani da Allah da manzonsa a duniya.**

**(88) Yahudawa da Nasara da wasu Mushirikai sun ce Allah Mai rahama ya riqi xa!.**

**(89) Lallai – Ya ku masu faxar wannan magana - kun zo da wani abu (na zance) mai girman gaske!.**

**(90) Saura qiris sammai su tsatsage, qasa ta kekkece, saboda munin wannan zance, haka nan saura qiris duwatsu su faffaxi su wargaje!**

**(91) Duk saboda sun jingina wa Allah mai rahama xa, Allah ya xaukaka daga barin haka xaukaka mai girma.**

**(92) Ba zai zama daidai ba, Allah mai rahama ya riqi xa, saboda ya tsarkaka daga hakan!.**

**(93) Duk wanda yake cikin sammai na daga Mala’iku da mutane da aljanu zasu je wajen Allah a ranar alqiyama suna masu qanqan da kai.**

**(94) Haqiqa ya kewaye su da iliminsa, ya kuma qididdige su matuqar qididdigewa, don haka babu abin da yake voyuwa a gare shi.**

**(95) Kuma kowa a cikinsu zai zo masa ne, shi kaxai, a ranar alqiyama, tilo, ba mataimaki, ba dukiya.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Ayoyin suna nuna wautar kafiri da raunin tunaninsa, da yawan yin burinsa na kayan daxi, alhali kuwa zai gamu da kishiyar haka xin ne a rayuwar lahira. 2 - Allah ya xora shaixanu akan kafirai, sun vatar da su, su ziga su, sun aikata sharri da savo. 3 - Mutanen masu falala da ilimi da nagarta za su yi ceto da izinin Allah a ranar alqiyama.**

إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ سَيَجۡعَلُ لَهُمُ
ٱلرَّحۡمَٰنُ وُدّٗا ٩٦ فَإِنَّمَا يَسَّرۡنَٰهُ بِلِسَانِكَ لِتُبَشِّرَ بِهِ
ٱلۡمُتَّقِينَ وَتُنذِرَ بِهِۦ قَوۡمٗا لُّدّٗا ٩٧ وَكَمۡ أَهۡلَكۡنَا قَبۡلَهُم
مِّن قَرۡنٍ هَلۡ تُحِسُّ مِنۡهُم مِّنۡ أَحَدٍ أَوۡ تَسۡمَعُ لَهُمۡ رِكۡزَۢا ٩٨

آياتها ١٣٥ سُورَةُ طه ترتيبها ٢٠

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

طه ١ مَآ أَنزَلۡنَا عَلَيۡكَ ٱلۡقُرۡءَانَ لِتَشۡقَىٰٓ ٢ إِلَّا تَذۡكِرَةٗ (الحزب ٣٢)
لِّمَن يَخۡشَىٰ ٣ تَنزِيلٗا مِّمَّنۡ خَلَقَ ٱلۡأَرۡضَ وَٱلسَّمَٰوَٰتِ ٱلۡعُلَى ٤
ٱلرَّحۡمَٰنُ عَلَى ٱلۡعَرۡشِ ٱسۡتَوَىٰ ٥ لَهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي
ٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَيۡنَهُمَا وَمَا تَحۡتَ ٱلثَّرَىٰ ٦ وَإِن تَجۡهَرۡ بِٱلۡقَوۡلِ
فَإِنَّهُۥ يَعۡلَمُ ٱلسِّرَّ وَأَخۡفَى ٧ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۖ لَهُ ٱلۡأَسۡمَآءُ
ٱلۡحُسۡنَىٰ ٨ وَهَلۡ أَتَىٰكَ حَدِيثُ مُوسَىٰٓ ٩ إِذۡ رَءَا نَارٗا
فَقَالَ لِأَهۡلِهِ ٱمۡكُثُوٓاْ إِنِّيٓ ءَانَسۡتُ نَارٗا لَّعَلِّيٓ ءَاتِيكُم مِّنۡهَا بِقَبَسٍ
أَوۡ أَجِدُ عَلَى ٱلنَّارِ هُدٗى ١٠ فَلَمَّآ أَتَىٰهَا نُودِيَ يَٰمُوسَىٰٓ ١١ إِنِّيٓ
أَنَا۠ رَبُّكَ فَٱخۡلَعۡ نَعۡلَيۡكَ إِنَّكَ بِٱلۡوَادِ ٱلۡمُقَدَّسِ طُوٗى ١٢



**96 Haqiqa waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka aikata ayyuka nagari, waxanda Allah ya yarda da su, to da sannu Allah zai saka musu wata soyayya a dalilin son sa da su, da kuma saka soyayyarsu a zukatan bayinsa.**

**97 Kaxai mun sauwaqe wannan Alqur'anin ne, ta hanyar saukar da shi da harshenka – Ya kai wannan Manzo - saboda ka yi albishir da shi ga masu jin tsoron Allah, waxanda suke kamanta umarnina da nisantar abubuwan da na hana, kuma ka tsoratar da mutanen da suke da tsananin jayayya da girman kai ga gaskiya.**

**98 Kuma al'ummu guda nawa ne muka halakar da su kafin mutanenka! Shi kana jin labarin wani daga cikin waxancan al'ummun, ko kana jin wani sauti na su voyayye?!. To abin da ya faru da su fa yana iya faruwa da wasunsu, duk lokacin da Allah ya yi izinin faruwar hakan.**

# Suratu Xaha

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Karfafa gwiwar Annabi (S.A.W) wajen xaukar nauyin isar da saqon da aka ba shi, da yin haquri a kan haka.**

## Tafsir:

**1 (Xaa Ha): Bayani ya gabata dangane da ire-iren waxannan haruffa a farkon Suratul Baqara.**

**2 Ba mu saukar maka da Alqur'ani ba – Ya kai wannan Manzo- don ya zamar maka sababin wahalar da kanka, da baqin ciki akan bijirewar da mutanenka suka yi na qin imani da shi.**

**3 Ba mu saukar da shi ba face sai don ya zama tunatarwa ga waxanda Allah ya yi musu dace da jin tsoronsa.**

**4 Allah wanda ya halicci qassai da Sammai maxaukaka shi ne ya saukar da shi, shi Alqur'ani ne mai girma, saboda ya sauka daga wurin Allah mai girma.**

**5 Mai Rahama ya xaukaka akan Al'arshi, xaukaka irin wadda da dace da girmansa, mai tsarki da xaukaka.**

**6 Abin da yake cikin Sammai da qassai da abin da yake qarqashin qasa na halittu duka nasa ne, shi kaxai, tsarki ya tabbata a gare shi, halittarsa ce, mulkinsa ne, gudanawarsa ce.**

**7 In ka bayyana zance – Ya kai wannan Manzo- ko ka yi shi voye, to duka dai, Allah mai tsarki yana sane da shi, don yana sane da sirri da abin da yafi sirri voyuwa, irin tunanin zuciya, babu abin da yake vuya a gare shi.**

**8 Allah shi ne wanda babu wani abin bauta bisa cancanta koma bayansa. Shi ne kaxai mai sunannaki waxanda suka kai matuqa wajen kyau. Yayin da Annabi (S.A.W) yake fama da bijirewar mutanensa sai Allah ya lallashe shi da labarin Annabi Musa (S.A.W). Allah ya ce:**

**9 Haqiqa labarin Annabi Musa xan Imrana (A.S) ya zo maka ya kai wannan Annabi.**

**10 Yayin da ya ga wata wuta a tafiyarsa da daddare, sai ya ce wa iyalansa: "Ku tsaya wurin da kuke, na ga wata wuta, wataqila in kawo muku makamashi daga gare ta, ko kuma in samu wani wanda zai nuna mini hanya".**

**11 Yayin da ya isa wurin wutar, sai Allah tsarki ya tabbata a gare shi ya kira shi, ya ce: "Ya Musa".**

**12 Haqiqa ni ne Ubangijinka, ka cire takalmanka, don ganawa da ni. Lallai yanzu kana wurin wani kwari ne mai tsarki, (Wanda ake kira Xuwa).**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Ba an saukar da Alqur'ani ba ne domin a gajiyar da kai wajen bauta, da xanxanawa kai xan wahala ba. Kaxai shi littafi ne na tunatarwa ga wanda masu tsoron Allah suke amfana da shi. 2 - Allah ya haxa tsakanin halitta da umarni, kamar yadda halitta akwai hikima a cikinta, to haka Allah ba ya yin umarni ko hani face sai don abin da yake ciki na adalci da hikima. 3 - Wajibi ne akan mai gida ya xauki nauyin iyalansa (matarsa) ciyarwa da tufatarwa da wurin zama, da kayan xumama xaki a lokacin sanyi.**

وَأَنَا ٱخْتَرْتُكَ فَٱسْتَمِعْ لِمَا يُوحَىٰٓ ١٣ إِنَّنِيٓ أَنَا ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠
فَٱعْبُدْنِي وَأَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ لِذِكْرِيٓ ١٤ إِنَّ ٱلسَّاعَةَ ءَاتِيَةٌ
أَكَادُ أُخْفِيهَا لِتُجْزَىٰ كُلُّ نَفْسِۭ بِمَا تَسْعَىٰ ١٥ فَلَا يَصُدَّنَّكَ
عَنْهَا مَن لَّا يُؤْمِنُ بِهَا وَٱتَّبَعَ هَوَىٰهُ فَتَرْدَىٰ ١٦ وَمَا تِلْكَ
بِيَمِينِكَ يَٰمُوسَىٰ ١٧ قَالَ هِيَ عَصَايَ أَتَوَكَّؤُاْ عَلَيْهَا
وَأَهُشُّ بِهَا عَلَىٰ غَنَمِي وَلِيَ فِيهَا مَـَٔارِبُ أُخْرَىٰ ١٨ قَالَ أَلْقِهَا
يَٰمُوسَىٰ ١٩ فَأَلْقَىٰهَا فَإِذَا هِيَ حَيَّةٞ تَسْعَىٰ ٢٠ قَالَ خُذْهَا
وَلَا تَخَفْۖ سَنُعِيدُهَا سِيرَتَهَا ٱلْأُولَىٰ ٢١ وَٱضْمُمْ يَدَكَ
إِلَىٰ جَنَاحِكَ تَخْرُجْ بَيْضَآءَ مِنْ غَيْرِ سُوٓءٍ ءَايَةً أُخْرَىٰ ٢٢ لِنُرِيَكَ
مِنْ ءَايَٰتِنَا ٱلْكُبْرَى ٢٣ ٱذْهَبْ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ إِنَّهُۥ طَغَىٰ ٢٤ قَالَ
رَبِّ ٱشْرَحْ لِي صَدْرِي ٢٥ وَيَسِّرْ لِيٓ أَمْرِي ٢٦ وَٱحْلُلْ عُقْدَةً مِّن
لِّسَانِي ٢٧ يَفْقَهُواْ قَوْلِي ٢٨ وَٱجْعَل لِّي وَزِيرًا مِّنْ أَهْلِي ٢٩ هَٰرُونَ
أَخِي ٣٠ ٱشْدُدْ بِهِۦٓ أَزْرِي ٣١ وَأَشْرِكْهُ فِيٓ أَمْرِي ٣٢ كَيْ نُسَبِّحَكَ
كَثِيرًا ٣٣ وَنَذْكُرَكَ كَثِيرًا ٣٤ إِنَّكَ كُنتَ بِنَا بَصِيرًا ٣٥ قَالَ قَدْ
أُوتِيتَ سُؤْلَكَ يَٰمُوسَىٰ ٣٦ وَلَقَدْ مَنَنَّا عَلَيْكَ مَرَّةً أُخْرَىٰٓ ٣٧



**13 Kuma na zave ka – Ya kai Musa- domin isar da saqo na, soboda haka ka saurari abin da zan yi maka wahayinsa.**

**14 "Haqiqa ni ne Allah, babu wani abin bauta da gaskiya sai ni. Ka bauta min ni kaxai, kuma ka tsayar da salla akan mafi kamalar siffa domin ka ambace ni (ko ka tuna da ni) a cikinta".**

**15 Haqiqa alqiyama tana nan tafe, babu makawa sai ta faru, Saura qiris in voye ta, don haka babu wani mahalukin da ya san lokacinta, sai dai sun san alamominta ta hanyar labarin da Annabi zai ba su (za ta tsaya) domin a saka wa kowace rai da abin da ta aikata, sawa'un na alheri ne ko na sharri.**

**16 "Kada wanda bai yi imani da ita ba daga cikin kafirai, wanda ya bi abin da zuciyarsa take so na haramun, ya kawar da kai daga bayar da gaskiya da ita, da yi mata shiri da ayyuka nagari, sai ka halaka saboda haka".**

**17 "Menene wancan a hannunka na dama ya kai Musa?".**

**18 Sai Annabi Musa (A.S) ya ce: Sandata ce, ina dogara a kanta yayin tafiya, kuma ina buga bishiya ta ita, domin ganyenta ya faxo ga awaki na, kuma dai tana min wasu amfani ban da waxannan da na ambata".**

**19 Sai Allah ya ce: "Jefar da ita, ya kai Musa".**

**20 Sai Annabi Musa ya jefar da ita, sai ta riqixe ta zama maciji tana tafiya da sauri kuma cikin sauki.**

**21 Sai Allah ya ce wa Annabi Musa (A.S): "Xauki sandarka, kar ka ji tsoron riqixewarta zuwa maciji, zamu mayar da ita, in ka xauke ta zuwa yanayinta na farko".**

**22 Kuma ka sa hannunka a cikin gefenka, zai fito fari fat, wannan ma wata aya ce ta biyu a gare ka".**

**23 "Mun nuna maka waxannan alamomi guda biyu ne, don mu nuna maka – Ya kai Musa - wasu daga cikin manya-manyan alamominmu, masu nuni akan ikonmu, da kuma nuni bisa cewa kai Manzo ne daga wurin Allah".**

**24 "Ka tafi – Ya kai Musa- zuwa ga Fir'auna, domin lallai shi ya qetare iyaka cikin kafirci da kangarewa Allah".**

**25 Sai Annabi Musa (A.S) ya ce: "Ya Ubangijina, ka yalwata mini qirji na, don na iya jure wa cutarwa".**

**26 "Kuma ka sauqaqa mini lamari na". 27 "Kuma ka bani ikon yin furuci da zance na fasaha".**

**28 "Domin du fahimci magana ta idan na isar musu da saqonka".**

**29 "Kuma ka sanya mini wani mataimaki daga cikin dangina, ya agaza mini cikin lamura na".**

**30 "Haruna xan Imrana, xan 'uwana". 31 "Ka qarafa mini gwiwa da shi".**

**32 "Kuma ka sa shi ya yi tarayya da ni cikin Manzanci"**

**33 "Don mu yi maka tasbihi mai yawa (wato mu tsarkake ka sosai)".**

**34 "Kuma mu ambace ka, ambato mai yawa".**

**35 "Lallai kai ka kasance dangane da mu, mai matugar gani da sani ne, babu wani abu cikin lamarinmu mai vuya a gare ka". 36 Sai Allah ya ce: "Mun baka abin da ka roqa, ya kai Musa".**

**37 "Kuma tabbas mun yi maka wata ni'ma a karo na biyu".**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Wajibcin kyakkyawan sauraro a cikin muhimman al'amura, mafi mahimmancin su kuwa shi ne wahayin da aka saukar daga wurin Allah.**

**2 - Farkon wahayi zuwa ga Annabi Musa (A.S) ya qunshi ginshiqai na aqida guda biyu, su ne: Yarda da kaxaitakar Allah, da imani da ranar alqiyama. Kuma ya qunshi mafi muhimmancin farillai bayan imani, shi ne sallah.**

**3 - Taimakekeniya tsakanin masu da'awa dole ne, domin samun nasara da cin ma manufa, ga shi Allah ya sanya wa Annabi Musa xan 'uwansa Haruna ya zama Annabi, domin ya taimaka mishi wajen isar da saqo.**

**4 - Mahimmancin mai da'awa ya mallaki qwarewa wajen fahimtar da wanda yake isar musu da da'awar.**

إِذۡ أَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰٓ أُمِّكَ مَا يُوحَىٰٓ ٣٨ أَنِ ٱقۡذِفِيهِ فِي ٱلتَّابُوتِ فَٱقۡذِفِيهِ
فِي ٱلۡيَمِّ فَلۡيُلۡقِهِ ٱلۡيَمُّ بِٱلسَّاحِلِ يَأۡخُذۡهُ عَدُوّٞ لِّي وَعَدُوّٞ لَّهُۥۚ وَأَلۡقَيۡتُ
عَلَيۡكَ مَحَبَّةٗ مِّنِّي وَلِتُصۡنَعَ عَلَىٰ عَيۡنِيٓ ٣٩ إِذۡ تَمۡشِيٓ أُخۡتُكَ فَتَقُولُ
هَلۡ أَدُلُّكُمۡ عَلَىٰ مَن يَكۡفُلُهُۥۖ فَرَجَعۡنَٰكَ إِلَىٰٓ أُمِّكَ كَيۡ تَقَرَّ عَيۡنُهَا
وَلَا تَحۡزَنَۚ وَقَتَلۡتَ نَفۡسٗا فَنَجَّيۡنَٰكَ مِنَ ٱلۡغَمِّ وَفَتَنَّٰكَ فُتُونٗاۚ
فَلَبِثۡتَ سِنِينَ فِيٓ أَهۡلِ مَدۡيَنَ ثُمَّ جِئۡتَ عَلَىٰ قَدَرٖ يَٰمُوسَىٰ ٤٠
وَٱصۡطَنَعۡتُكَ لِنَفۡسِي ٤١ ٱذۡهَبۡ أَنتَ وَأَخُوكَ بِـَٔايَٰتِي وَلَا
تَنِيَا فِي ذِكۡرِي ٤٢ ٱذۡهَبَآ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ إِنَّهُۥ طَغَىٰ ٤٣ فَقُولَا لَهُۥ قَوۡلٗا
لَّيِّنٗا لَّعَلَّهُۥ يَتَذَكَّرُ أَوۡ يَخۡشَىٰ ٤٤ قَالَا رَبَّنَآ إِنَّنَا نَخَافُ أَن يَفۡرُطَ
عَلَيۡنَآ أَوۡ أَن يَطۡغَىٰ ٤٥ قَالَ لَا تَخَافَآۖ إِنَّنِي مَعَكُمَآ أَسۡمَعُ وَأَرَىٰ
٤٦ فَأۡتِيَاهُ فَقُولَآ إِنَّا رَسُولَا رَبِّكَ فَأَرۡسِلۡ مَعَنَا بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ
وَلَا تُعَذِّبۡهُمۡۖ قَدۡ جِئۡنَٰكَ بِـَٔايَةٖ مِّن رَّبِّكَۖ وَٱلسَّلَٰمُ عَلَىٰ مَنِ ٱتَّبَعَ
ٱلۡهُدَىٰٓ ٤٧ إِنَّا قَدۡ أُوحِيَ إِلَيۡنَآ أَنَّ ٱلۡعَذَابَ عَلَىٰ مَن كَذَّبَ
وَتَوَلَّىٰ ٤٨ قَالَ فَمَن رَّبُّكُمَا يَٰمُوسَىٰ ٤٩ قَالَ رَبُّنَا ٱلَّذِيٓ أَعۡطَىٰ
كُلَّ شَيۡءٍ خَلۡقَهُۥ ثُمَّ هَدَىٰ ٥٠ قَالَ فَمَا بَالُ ٱلۡقُرُونِ ٱلۡأُولَىٰ ٥١



**38 Yayin da muka kimsa wa mahaifiyarka abin da muka kimsa mata, don kare ka daga makircin Fir'auna. 39 Haqiqa mun umarce ta ya yi da muka kimsa mata cewa: "Bayan kin haife shi ki jefa shi a cikin akwati, ki jefa akwatin a cikin teku, tekun zai jefa shi bakin gava da umarninmu. Sai maqiyina kuma maqiyin shi ya xauke shi, wanda shi ne Fir'auna". Hakanan na sanya maka wata soyayya daga gare ni, sai mutane suka so ka, don a rene ka akan idanu na, cikin kariya na da kulawata. 40 Yayin da 'yar uwarka ta fito tana ta tafiya, duk inda akwatin ya yi, tana bin sa, sai ta cewa waxanda suka xauke shi: "Shin in nuna muka wadda zata kula da shi, ta shayar da shi, ta raine shi?". Sai Muka yi maka ni'ma da mayar da kai zuwa wajen mahaifiyarka, don ta yi farin ciki da komowarka zuwa wurinta, kuma don kada ta yi baqin cikin rashinka, Kuma ka kashe Baqibxen da ka naushe shi, amma muka yi maka ni'imar tserar da kai daga uquba. Mun tserar da kai, ba sau xaya ba, ba sau biyu ba, a duk lokacin da ka shiga cikin wata jarrabawa, har ka fita daga garin, ka zauna a wurin mutanen Madyana na wasu shekaru, sannan ka dawo a lokacin da aka qaddara maka ka dawo, domin na yi magana da kai, ya kai Musa. 41 Kuma Na zave ka ga kaina, a matsayin Manzona, domin ka isar da saqona zuwa ga mutane.**

**42 Ka tafi kai – Musa - da xan uwanka Haruna da ayoyina, masu nuni ga ikon Allah da kaxaitakarsa, kuma kar ku yi rauni wajen kira zuwa gare ni, da yawan ambatona.**

**43 Ku tafi zuwa ga Fir'auna, domin lallai ya wuce gona da iri, wurin kafirci da kangarewa ga Allah.**

**44 Ku faxa masa zance mai taushi, wanda babu kaushi cikinsa, da fatan ya yi tunani ko ya ji tsoron Allah ya tuba.**

**45 Annabi Musa da Annabi Haruna (A.S) suka ce: "Lallai mu, muna jin tsoron kar ya gaggauta yi mana uquba, tun kafin mu gama isar masa da saqon, ko kuma ya zarce iyaka cikin zaluntarmu, ya kashe mu, ko dai wani abu haka".**

**46 Sai Allah ya ce musu: "Kar ku ji tsoro, lallai ni ina tare da ku da kiyayewa ta, da qarfafa muku gwiwa, kuma ina ji, ina ganin abin da zai faru tsakaninku da shi".**

**47 "Ku je wurinsa, ku ce masa: "Mu 'yan aiken Ubangijinka ne – Ya kai Fir'auna -, don haka ka bamu Bani-Isra'ila, kar ka azabtar da su ta hanyar kashe 'ya'yansu maza da barin 'ya'yansu mata, lallai mun zo maka da hujja daga wurin Ubangijinmu akan gaskiyarmu, Amincin Allah ya tabbata akan duk wanda ya yi imani, ya bi shiriyar Allah". 48 "Lallai mu an yi mana wahayin cewa lallai azaba a duniya da lahira zata tabbata ga duk wanda ya qaryata ayoyin Allah, ya juya baya ga abin da Manzanni suka zo da shi".**

**49 Sai Fir'auna ya ce, yana mai inkarin abin da suka zo da shi: "To waye Ubangijin naku da kuke riyawa cewa shi ya aiko ku zuwa gare ni, ya kai Musa?".**

**50 Sai Annabi Musa (A.S) ya ce: "Ubangijinmu shi ne wanda ya bai wa komai kamanninsa yadda ya dace da shi, sannan ya shiryar da ababen halitta zuwa ga abin da ya halitta musu".**

**51 Sai Fir'auna ya ce: "To yaya lamarin al'ummun da suka gabata, waxanda suka kasance akan kafirci?".**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Cikar kulawar Allah ga wanda ya yi magana da shi, wato Annabi Musa (A.S), da sauran Annabawa da Manzanni. Haka ma Magadansu ma suna da wani kaso na wannan kulawar, gwargwadon matsayinsu a wurin Allah. 2 - Yana daga cikin shiryarwa ta gaba xaya ga halittu, ka ga kowane abin halitta yana gaggawa zuwa ga abin da aka halitta masa na amfani, da kawar da duk abin da zai cuce shi. 3 - Bayanin falalar umarni da kyakkyawa da hani da mummuna, ta hanyar tausasa magana daga wanda aka ba kariya zuwa ga wanda yake da qarfi. 4 - Allah shi ne wanda ya kevanta da sanin abin da ya vuya ( wato gaibu) na da, da na yanzu, da na nan gaba.**

قَالَ عِلۡمُهَا عِندَ رَبِّي فِي كِتَٰبٖۖ لَّا يَضِلُّ رَبِّي وَلَا يَنسَى ٥٢ ٱلَّذِي
جَعَلَ لَكُمُ ٱلۡأَرۡضَ مَهۡدٗا وَسَلَكَ لَكُمۡ فِيهَا سُبُلٗا وَأَنزَلَ مِنَ
ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَأَخۡرَجۡنَا بِهِۦٓ أَزۡوَٰجٗا مِّن نَّبَاتٖ شَتَّىٰ ٥٣ كُلُواْ
وَٱرۡعَوۡاْ أَنۡعَٰمَكُمۡۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّأُوْلِي ٱلنُّهَىٰ ٥٤ ۞ مِنۡهَا
خَلَقۡنَٰكُمۡ وَفِيهَا نُعِيدُكُمۡ وَمِنۡهَا نُخۡرِجُكُمۡ تَارَةً أُخۡرَىٰ ٥٥ وَلَقَدۡ
أَرَيۡنَٰهُ ءَايَٰتِنَا كُلَّهَا فَكَذَّبَ وَأَبَىٰ ٥٦ قَالَ أَجِئۡتَنَا لِتُخۡرِجَنَا
مِنۡ أَرۡضِنَا بِسِحۡرِكَ يَٰمُوسَىٰ ٥٧ فَلَنَأۡتِيَنَّكَ بِسِحۡرٖ مِّثۡلِهِۦ
فَٱجۡعَلۡ بَيۡنَنَا وَبَيۡنَكَ مَوۡعِدٗا لَّا نُخۡلِفُهُۥ نَحۡنُ وَلَآ أَنتَ مَكَانٗا
سُوٗى ٥٨ قَالَ مَوۡعِدُكُمۡ يَوۡمُ ٱلزِّينَةِ وَأَن يُحۡشَرَ ٱلنَّاسُ ضُحٗى
٥٩ فَتَوَلَّىٰ فِرۡعَوۡنُ فَجَمَعَ كَيۡدَهُۥ ثُمَّ أَتَىٰ ٦٠ قَالَ لَهُم
مُّوسَىٰ وَيۡلَكُمۡ لَا تَفۡتَرُواْ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبٗا فَيُسۡحِتَكُم بِعَذَابٖۖ
وَقَدۡ خَابَ مَنِ ٱفۡتَرَىٰ ٦١ فَتَنَٰزَعُوٓاْ أَمۡرَهُم بَيۡنَهُمۡ وَأَسَرُّواْ
ٱلنَّجۡوَىٰ ٦٢ قَالُوٓاْ إِنۡ هَٰذَٰنِ لَسَٰحِرَٰنِ يُرِيدَانِ أَن يُخۡرِجَاكُم
مِّنۡ أَرۡضِكُم بِسِحۡرِهِمَا وَيَذۡهَبَا بِطَرِيقَتِكُمُ ٱلۡمُثۡلَىٰ ٦٣
فَأَجۡمِعُواْ كَيۡدَكُمۡ ثُمَّ ٱئۡتُواْ صَفّٗاۚ وَقَدۡ أَفۡلَحَ ٱلۡيَوۡمَ مَنِ ٱسۡتَعۡلَىٰ ٦٤

الحزب ٣٢



**(52) Sai Annabi Musa (A.S) ya ce wa Fir'auna: "Sanin abin da waxancan al'ummu suke ciki yana wurin Ubangijina, a tabbace a cikin Lauhul Mahfuz. Ubangijina baya kuskure cikin saninsu, kuma baya manta abin da ya sani a kansu".**
**(53) Yana wurin Ubangijina wanda ya sanya muku qasa ta zama shimfixaxxiya don a rayu a kanta, ya kuma sanya muka hanyoyi a kanta, waxanda za a iya tafiya a cikinsu, kuma ya saukar muku da ruwan sama daga sama, sai muka fitar da dangogin tsirrai daban daban, da wannan ruwan.**
**(54) Ku ci – Ya ku mutane- daga abin da muka fitar muku na daxaxan abubuwa, kuma ku yi kiwon dabbobinku a ciki. Lallai akwai ayoyi cikin abin da aka ambata xin nan, na ni'imomi akan ikon Allah da kaxaitakarsa ga masu hankali.**
**(55) Daga turvayar qasa muka halicci babanku Annabi Adam (A.S), kuma cikinta zamu mayar daku ta hanyar binnewa idan kun mutu, kuma daga cikinta zamu sake fitar da ku a wani karon, don tashin alqiyama.**
**(56) Lallai Mun nuna wa Fir'auna ayoyinmu guda taran nan dukkaninsu, ya gansu amma ya qaryata su, ya qi ya amsa kira zuwa ga imani da Allah.**
**(57) Fir'auna ya ce: "Shin ka zo mana ne domin ka fitar da mu daga qasar Misra da abin da ka zo da shi na sihirinka, don mulkin ta ya wanzu a gare ka, ya kai Musa?!".**
**(58) To lallai zamu kawo maka sihiri irin sihirinka –ya kai Musa-, ka sanya lokaci a tsakaninmu da kai, lokaci sananne da wuri kevantacce, ba zamu sava ba, kaima kar ka sava, kuma ya zama wuri ne tsaka-tsaki tsakanin vangarorin guda biyu".**
**(59) Sai Annabi Musa (A.S) ya ce wa Fir'auna: "Lokaci tsakaninmu da ku shi ne, ranar idi, lokacin da mutane suke haxuwa don bikin idi da hantsi".**
**(60) Sai fir'auna ya juya baya, ya tafi, ya gama haxa makircinsa da dabarunsa, sannan ya zo wurin da aka tsara akan lokacin da aka bayar, don samun galaba.**
**(61) Sai Annabi Musa (A.S) ya ce - yana mai yin wa'azi ga matsafan Fir'auna -: "Kar ku qagi qarya ku jingina wa Allah, da abin da kuke yaudarar mutane da shi na sihirinku. Idan kuka yi haka, sai Allah ya tumvuke ku da wata azaba daga wurinsa. Duk wanda ya qirqiri qarya ya jingina wa Allah ya yi hasara".**
**(62) Sai masu sihirin suka xan yi muhawara a tsakaninsu yayin da suka ji maganar Annabi Musa (A.S), suka gana da junansu a voye.**
**(63) Sai sashen masu sihiri suka cewa sashe: "Haqiqa Musa da Haruna masu sihiri ne, suna son su fitar da ku ne daga garin Misra da wannan tsafin na su, da suka zo da shi, su tafiyar da mafificin tsarinku na rayuwa da tafarkinku maxaukaki".**
**(64) "Ku kyautata lamarinku, kar ku yi savani cikinsa, sannan ku fito gaba xayanku cikin sahu xaya, ku jefa abin da ke wurinku a lokaci guda. Haqiqa duk wanda ya yi galaba akan abokin hamayyarsa yau, to shi ne mai rabo".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Fitar da kala-kalan tsirrai, masu bambancin kamanni da launi, daga qasa dalili ne bayyananne akan ikon Allah Maxaukakin Sarki da samuwar Ubangiji.**
**2 - Ayoyin sun ambaci dalilai guda biyu na hankali bayyanannu akan yiwuwar dawo da halitta bayan mutuwa, su ne: Fitar da tsirrai daga qasa bayan mutuwarta, da fitar da mutane da samuwarsu daga cikinta.**
**3 - Kafircin Fir'auna kafirci ne na taurin kai, domin ya ga ayoyi qiri qiri, ba labari aka ba shi ba, kuma ya yarda da su a cikin zuciyarsa. 4 - Annabi Musa (A.S) ya zavi ranar idi ne, don kalmar Allah ta xaukaka, addininsa ya yi galaba, kafirci ya daqile, a gaban mutane baki xaya, cikin taro na gama-gari, kuma saboda labari ya yaxu a ko'ina.**

قَالُوا۟ يَـٰمُوسَىٰٓ إِمَّآ أَن تُلْقِىَ وَإِمَّآ أَن نَّكُونَ أَوَّلَ مَنْ أَلْقَىٰ ٦٥ قَالَ بَلْ
أَلْقُوا۟ ۖ فَإِذَا حِبَالُهُمْ وَعِصِيُّهُمْ يُخَيَّلُ إِلَيْهِ مِن سِحْرِهِمْ أَنَّهَا
تَسْعَىٰ ٦٦ فَأَوْجَسَ فِى نَفْسِهِۦ خِيفَةً مُّوسَىٰ ٦٧ قُلْنَا لَا تَخَفْ إِنَّكَ
أَنتَ ٱلْأَعْلَىٰ ٦٨ وَأَلْقِ مَا فِى يَمِينِكَ تَلْقَفْ مَا صَنَعُوٓا۟ ۖ إِنَّمَا صَنَعُوا۟
كَيْدُ سَـٰحِرٍ ۖ وَلَا يُفْلِحُ ٱلسَّاحِرُ حَيْثُ أَتَىٰ ٦٩ فَأُلْقِىَ ٱلسَّحَرَةُ سُجَّدًا
قَالُوٓا۟ ءَامَنَّا بِرَبِّ هَـٰرُونَ وَمُوسَىٰ ٧٠ قَالَ ءَامَنتُمْ لَهُۥ قَبْلَ أَنْ ءَاذَنَ
لَكُمْ ۖ إِنَّهُۥ لَكَبِيرُكُمُ ٱلَّذِى عَلَّمَكُمُ ٱلسِّحْرَ ۖ فَلَأُقَطِّعَنَّ أَيْدِيَكُمْ
وَأَرْجُلَكُم مِّنْ خِلَـٰفٍ وَلَأُصَلِّبَنَّكُمْ فِى جُذُوعِ ٱلنَّخْلِ وَلَتَعْلَمُنَّ
أَيُّنَآ أَشَدُّ عَذَابًا وَأَبْقَىٰ ٧١ قَالُوا۟ لَن نُّؤْثِرَكَ عَلَىٰ مَا جَآءَنَا مِنَ
ٱلْبَيِّنَـٰتِ وَٱلَّذِى فَطَرَنَا ۖ فَٱقْضِ مَآ أَنتَ قَاضٍ ۖ إِنَّمَا تَقْضِى هَـٰذِهِ
ٱلْحَيَوٰةَ ٱلدُّنْيَآ ٧٢ إِنَّآ ءَامَنَّا بِرَبِّنَا لِيَغْفِرَ لَنَا خَطَـٰيَـٰنَا وَمَآ أَكْرَهْتَنَا
عَلَيْهِ مِنَ ٱلسِّحْرِ ۗ وَٱللَّهُ خَيْرٌ وَأَبْقَىٰٓ ٧٣ إِنَّهُۥ مَن يَأْتِ رَبَّهُۥ مُجْرِمًا
فَإِنَّ لَهُۥ جَهَنَّمَ لَا يَمُوتُ فِيهَا وَلَا يَحْيَىٰ ٧٤ وَمَن يَأْتِهِۦ مُؤْمِنًا قَدْ
عَمِلَ ٱلصَّـٰلِحَـٰتِ فَأُو۟لَـٰٓئِكَ لَهُمُ ٱلدَّرَجَـٰتُ ٱلْعُلَىٰ ٧٥ جَنَّـٰتُ عَدْنٍ
تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَـٰرُ خَـٰلِدِينَ فِيهَا ۚ وَذَٰلِكَ جَزَآءُ مَن تَزَكَّىٰ ٧٦



**(65) Sai masu sihiri suka ce wa Annabi Musa (A.S): "Ya kai Musa, ka zavi xayan biyu: "Ko fara jefa abin da ka zo da shi na tsafi, ko kuma mu, mu zama farkon waxanda za su jefa".**
**(66) Sai Annabi Musa (A.S) ya ce: "A'a, ku fara jefa abin da ke wurinku". Sai suka jefa abin da zuka zo da shi. Sai ga igiyoyinsu da sandunansu da suka jefa ana surantawa Annabi Musa kamar sun zama macizai, suna motsawa da sauri, a sakamakon tsafinsu".**
**(67) Sai Annabi Musa (A.S) ya ji tsoro cikin abin da suka yi a zuciyarsa, amma bai bayyana tsoron ba.**
**(68) Sai Allah Maxaukin Sarki ya ce wa Annabi Musa (A.S), yana kwantar masa da rai cewa: "Kar ka ji tsoron abin da aka suranta maka, Tabbas kai – Ya Musa- kai ne a sama da su, za ka yi nasara da galaba a kansu".**
**(69) "Ka jefa sandarka dake hannun damanka, za ta rikixe ta zama macijiya, kuma zata haxiye abin da suka yi na tsafi. Ai ba wani abu suka yi ba face dabara ce ta tsafi, kuma matsafi ba zai yi nasara ba a duk inda yake".**
**(70) Sai Annabi Musa (A.S) ya jefa sandarsa, sai ta rikixe ta zama macijiya, kuma ta haxiye duk abin da matsafan nan suka yi, sai matsafa suka faxi suka yi sujjada ga Allah, saboda masaniyarsu cewa abin da Annabi Musa (A.S) ya zo da shi ba tsafi bane, tabbas daga wurin Allah yake. Suka ce: "Mun yi imani da Ubangijin Musa da Haruna, Ubangijin talikai gaba xaya".**
**(71) Sai Fir'auna ya ce - yana mai inkari da gargaxi ga matsafan akan imaninsu -: "Shin kun yi imani da Musa ne tun kafin na baku izinin yin hakan?! Lallai – Ya ku Matsafa - Musa shi ne shugabanku, wanda ya koya muku tsafi, to lallai sai na yanyanke hannu da qafar kowa a cikinku, ta gefe daban-daban, kuma sai na tsire ku a kan kututturen dabino har ku mutu, don ku zama abin izina ga wasunku, kuma lallai lokacin zaku san waye ya fi tsanani da dauwamar uquba, ni ne ko Ubangijin Musa!".**
**(72) Sai Masu sihirin nan suka ce wa Fir'auna: "Ba zamu tava fifita biyayya a gareka ba – Ya kai Fir'auna- sama da biyayya ga abin da ya zo mana na ayoyi bayyanannu. Kuma ba zamu tava fifita ka akan Allah wanda ya halicce mu ba. Ka yi duk abin da za ka yi da mu, baka da wani iko a kanmu sai dai a wanna rayuwa ta duniya mai gushewa, kuma ikonka zai gushe". (73) "Haqiqa mu, mun yi imani da Ubangijinmu ne don fatan ya shafe mana kurakuranmu na kafirci da sauransu, kuma ya yafe mana zunubin tsafin da ka tilasta mana koyonsa da yin sa, da kuma faxa da Musa da shi. Ladan Allah yafi alheri sama da ladan da ka yi mana alqawarinsa, kuma azabar Allah ta fi wanzuwa sama da gargaxin da ka yi mana na azaba". (74) Yadda lamarin yake shi ne: duk wanda ya je wa Ubangijinsa a ranar alqiyama yana kafiri, to yana da wutar Jahannama, zai shiga cikinta, ya zauna zama na din-din-din, ba zai mutu a ciki ba, ballantana ya huta daga azabarta, kuma ba zai rayu rayuwa mai kyau ba. (75) Kuma duk wanda ya je wa Ubangijinsa a ranar alqiyama yana mumini, kuma ya aikata ayyuka nagari, to masu siffantuwa da waxannan manyan siffofin suna da manyan matsayi da matakai na qoli. (76) Waxannan matakan su ne: Aljannatai na zaman din-din-din, waxanda qoramu suke gudana ta qarqashin gine-ginensu, za su zauna a cikin har abada. Kuma wannan shi ne sakamakon duk wanda ya tsarkaka daga kafirci da savo.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Mai sihiri ba zai tsira ba a duk inda ya shiga a bayan qasa, duk dabararsa, kuma buqatarsa ta alheri ko ta sharri, ba zata tava biya ba da sihiri da tsafi.**
**2 - Imani yana haifar da mu'u'jizozi. Ga shi imanin matsafan nan ya tabbata kamar duwatsu, ya sa azabar duniya ta zama ba komai ba a wurinsu, kuma ba su damu da barazanar Fir'auna ba.**
**3 - Al'adar masu girman kai ce su yi barazanar azaba mai tsanani ga masu gaskiya, kuma su wuce gona da iri, cikin wannan barazanar domin qasqantarwa da wulakanci a gare su.**

وَلَقَدۡ أَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰ مُوسَىٰٓ أَنۡ أَسۡرِ بِعِبَادِي فَٱضۡرِبۡ لَهُمۡ طَرِيقٗا
فِي ٱلۡبَحۡرِ يَبَسٗا لَّا تَخَٰفُ دَرَكٗا وَلَا تَخۡشَىٰ ٧٧ فَأَتۡبَعَهُمۡ فِرۡعَوۡنُ
بِجُنُودِهِۦ فَغَشِيَهُم مِّنَ ٱلۡيَمِّ مَا غَشِيَهُمۡ ٧٨ وَأَضَلَّ فِرۡعَوۡنُ قَوۡمَهُۥ
وَمَا هَدَىٰ ٧٩ يَٰبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ قَدۡ أَنجَيۡنَٰكُم مِّنۡ عَدُوِّكُمۡ وَوَٰعَدۡنَٰكُمۡ
جَانِبَ ٱلطُّورِ ٱلۡأَيۡمَنَ وَنَزَّلۡنَا عَلَيۡكُمُ ٱلۡمَنَّ وَٱلسَّلۡوَىٰ ٨٠ كُلُواْ مِن
طَيِّبَٰتِ مَا رَزَقۡنَٰكُمۡ وَلَا تَطۡغَوۡاْ فِيهِ فَيَحِلَّ عَلَيۡكُمۡ غَضَبِيۖ
وَمَن يَحۡلِلۡ عَلَيۡهِ غَضَبِي فَقَدۡ هَوَىٰ ٨١ وَإِنِّي لَغَفَّارٞ لِّمَن تَابَ
نصف الحزب ٣٢ وَءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحٗا ثُمَّ ٱهۡتَدَىٰ ٨٢ ۞ وَمَآ أَعۡجَلَكَ عَن
قَوۡمِكَ يَٰمُوسَىٰ ٨٣ قَالَ هُمۡ أُوْلَآءِ عَلَىٰٓ أَثَرِي وَعَجِلۡتُ إِلَيۡكَ
رَبِّ لِتَرۡضَىٰ ٨٤ قَالَ فَإِنَّا قَدۡ فَتَنَّا قَوۡمَكَ مِنۢ بَعۡدِكَ وَأَضَلَّهُمُ
ٱلسَّامِرِيُّ ٨٥ فَرَجَعَ مُوسَىٰٓ إِلَىٰ قَوۡمِهِۦ غَضۡبَٰنَ أَسِفٗاۚ قَالَ
يَٰقَوۡمِ أَلَمۡ يَعِدۡكُمۡ رَبُّكُمۡ وَعۡدًا حَسَنًاۚ أَفَطَالَ عَلَيۡكُمُ ٱلۡعَهۡدُ
أَمۡ أَرَدتُّمۡ أَن يَحِلَّ عَلَيۡكُمۡ غَضَبٞ مِّن رَّبِّكُمۡ فَأَخۡلَفۡتُم
مَّوۡعِدِي ٨٦ قَالُواْ مَآ أَخۡلَفۡنَا مَوۡعِدَكَ بِمَلۡكِنَا وَلَٰكِنَّا حُمِّلۡنَآ
أَوۡزَارٗا مِّن زِينَةِ ٱلۡقَوۡمِ فَقَذَفۡنَٰهَا فَكَذَٰلِكَ أَلۡقَى ٱلسَّامِرِيُّ ٨٧



**(77) Kuma lallai mun yi wahayi zuwa ga Annabi Musa cewa: “Ka tafi da bayi na cikin dare, ku fita daga Misra, kar wani ya gane ku, kuma ka samar musu hanya busasshiya a cikin teku, bayan ka daki tekun da sandarka, kana cikin aminci ba ka jin tsoron Fir'auna da 'yan kanzaginsa su riske ku, kuma ba ka jin tsoron nutsewa cikin teku.**

**(78) Sai Fir'auna ya bi bayansu, shi da sojojinsa, sai tekun ya haxiye shi da rundunar sojojinsa da abin da babu wanda ya san haqiqaninsa sai Allah, sai suka nitse gaba xayansu, suka halaka. Annabi Musa kuma ya tsira da waxanda suke tare da shi.**

**(79) Fir'auna ya vatar da mutanensa sakamakon abin da yake qawata musu na kafirci, ya yaudare su da qarya, bai shiryar da su zuwa tafarkin shiriya ba.**

**(80) Mun faxa wa bani Isra'ila bayan mun kuvutar da su daga Fir'auna da rundunarsa cewa: “Ya ku Bani Isra'ila, lallai mun kuvutar da ku daga hannun abokin gabarku, kuma mun yi muku alqawarin zamu yi magana da Musa a vangaren damar kwarin da yake gefen daman dutsen Sina, kuma Mun saukar muku da abin sha mai zaqi, a lokacin fagamniyarku, irin su zuma da tsuntsun nan xan qarami mai daxin nama, mai kama da fakara.**

**(81) Ku ci daxaxan abubuwan da muka azurta ku da su na abincin halal. Kar ku qetare haddin abin da muka halasta muku zuwa ga abin da muka haramta muku, don sai fushi na ya sauka a kanku, duk wanda fushi na ya sauka a kansa to ya halaka, ya tave a duniya da lahira.**

**(82) Kuma lallai ni mai yawan gafara da yafiya ne ga wanda ya tuba zuwa gare ni, ya yi imani, kuma ya aikata aiki**
**nagari sannan kuma ya tsayu qyam a kan gaskiya. (83) “Me yasa ka yi gaggawa – Ya kai Musa- ka yi gaba ka bar**
**mutanenka a baya?”. (84) Annabi Musa (A.S) ya ce: “Ga su nan a bayana, za su tarar da ni, na yi gaggawa na riga**
**su zuwa gareka ne, domin ka yarda da ni saboda gaggawata zuwa gare ka”.**

**(85) Sai Allah ya ce: “To lallai mun jarrabi mutanenka waxanda ka baro su a bayanka, da bautar xan maraqi, haqiqa Samiriyu ne ya kira su zuwa ga bautarsa, ya vatar da su da hakan”.**

**(86) Sai Annabi Musa (A.S) ya dawo wurin mutanensa cikin fushi, saboda bautar xan maraqi da suka yi, yana cikin baqin ciki, ya ce: “Ya ku mutane na, shin Allah bai yi muku kyakkyawan alqawari ba, ya saukar muku da Attaura, kuma ya shigar da ku Aljanna ba? Shin zamani ya yi muku tsawo ne har kuka manta?. Ko dai kawai kuna son fushin Ubangijinku ya sauka a kanku ne, azabarsa ta faxa a kanku, da wannan aika-aikan na ku, shi ya sa kuka sava alqawarina na tabbata akan biyayya, har na dawo zuwa gare ku?!”**

**(87) Sai mutanen Annabi Musa suka ce: “Ba mun sava alqawarinka ba ne – Ya kai Musa- da zavinmu. A'a, tilas ce ta sa haka, don an xora mana kayan nauyi na adon mutanen Fir'auna, sai muka jefar da su a rami, don mu kuvuta daga gare su. Kamar yadda muka jefa su a rami, haka Samiriyyu shi ma ya jefa abin da yake wurinsa na turvayar kofaton dokin Mala'ika Jibril (A.S).**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Yana daga cikin sunnar Allah, ya xau fansa akan masu laifi da abin da zai warkar da zukatan muminai, ya sanyaya musu ido, ya tafiyar musu da fushinsu. 2 - Shugaba xan ta'adda bala'i ne ga kansa da mutanensa, domin zai vatar da su daga shiriya, kuma ba zai nuna musu hanyar alheri ko ta tsira ba. 3 - Ni'imomi suna wajabta kiyaye su da godiya, wanda hakan yake jawo a qara su. Butulce wa ni'ima kuma yana ja wo saukar fushin Allah da afkuwarsa akan butulu. 4 - Allah mai cikakken gafara ne na din-din-din, ga duk wanda ya tuba daga shirka, da kafirci da savo, ya yi imani da shi, kuma ya yi aiki nagari, sannan ya tabbata a kan haka har ya mutu a kansa. 5 - Du da cewa gaggawa abin zargi ce a dunqule, amma dai abin yabo ce cikin ayyukan addini.**

فَأَخۡرَجَ لَهُمۡ عِجۡلٗا جَسَدٗا لَّهُۥ خُوَارٞ فَقَالُواْ هَٰذَآ إِلَٰهُكُمۡ
وَإِلَٰهُ مُوسَىٰ فَنَسِيَ ٨٨ أَفَلَا يَرَوۡنَ أَلَّا يَرۡجِعُ إِلَيۡهِمۡ قَوۡلٗا
وَلَا يَمۡلِكُ لَهُمۡ ضَرّٗا وَلَا نَفۡعٗا ٨٩ وَلَقَدۡ قَالَ لَهُمۡ هَٰرُونُ
مِن قَبۡلُ يَٰقَوۡمِ إِنَّمَا فُتِنتُم بِهِۦۖ وَإِنَّ رَبَّكُمُ ٱلرَّحۡمَٰنُ فَٱتَّبِعُونِي
وَأَطِيعُوٓاْ أَمۡرِي ٩٠ قَالُواْ لَن نَّبۡرَحَ عَلَيۡهِ عَٰكِفِينَ حَتَّىٰ يَرۡجِعَ
إِلَيۡنَا مُوسَىٰ ٩١ قَالَ يَٰهَٰرُونُ مَا مَنَعَكَ إِذۡ رَأَيۡتَهُمۡ ضَلُّوٓاْ ٩٢
أَلَّا تَتَّبِعَنِۖ أَفَعَصَيۡتَ أَمۡرِي ٩٣ قَالَ يَبۡنَؤُمَّ لَا تَأۡخُذۡ بِلِحۡيَتِي
وَلَا بِرَأۡسِيٓۖ إِنِّي خَشِيتُ أَن تَقُولَ فَرَّقۡتَ بَيۡنَ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ
وَلَمۡ تَرۡقُبۡ قَوۡلِي ٩٤ قَالَ فَمَا خَطۡبُكَ يَٰسَٰمِرِيُّ ٩٥ قَالَ
بَصُرۡتُ بِمَا لَمۡ يَبۡصُرُواْ بِهِۦ فَقَبَضۡتُ قَبۡضَةٗ مِّنۡ أَثَرِ
ٱلرَّسُولِ فَنَبَذۡتُهَا وَكَذَٰلِكَ سَوَّلَتۡ لِي نَفۡسِي ٩٦ قَالَ
فَٱذۡهَبۡ فَإِنَّ لَكَ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ أَن تَقُولَ لَا مِسَاسَۖ وَإِنَّ لَكَ
مَوۡعِدٗا لَّن تُخۡلَفَهُۥۖ وَٱنظُرۡ إِلَىٰٓ إِلَٰهِكَ ٱلَّذِي ظَلۡتَ عَلَيۡهِ
عَاكِفٗاۖ لَّنُحَرِّقَنَّهُۥ ثُمَّ لَنَنسِفَنَّهُۥ فِي ٱلۡيَمِّ نَسۡفًا ٩٧ إِنَّمَآ
إِلَٰهُكُمُ ٱللَّهُ ٱلَّذِي لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۚ وَسِعَ كُلَّ شَيۡءٍ عِلۡمٗا ٩٨



**(88) Sai Samiriyyu ya fitar wa da Bani Isra'ila wani gangar jikin xan maraqi, wanda ba shi da rai, amma yana qara kamar kukan shanu, daga cikin waxannan kayan adon, sai waxanda suka fitinu a cikinsu da wannan aiki na Samiriyyu suka ce: "Wannan shi ne abin bautarku, kuma abin bautar Musa, amma ya manta shi a nan".**

**(89) Shin waxannan waxanda suka fitinu da xan maraqi, har suka bauta masa, ba sa ganin cewa xan maraqin nan ba ya iya yi musu magana, ba ya iya amsa maganarsu, kuma ba zai iya tunkuxe musu ko waninsu wata cuta ba, ba zai iya jawo wa wanin sa ko kansa wani amfani ba?!"**

**(90) Kuma lallai Annabi Haruna (A.S) ya faxa musu tun kafin Annabi Musa (A.S) ya dawo wurinsu cewa: "Babu abin da yake cikin yin xan maraqi daga zinari, da saka shi ya yi qara face jarrabawa a gare ku, domin a gane mumini da kafiri, kuma haqiqa Ubangijinku – Ya ku mutane na - shi ne wanda ya mallaki rahama, ba wanda ba shi da ikon cutarwa ko amfanarwa a gare ku ba, ballantana ya yi muku rahama. Don haka ku yi mini biyayya wajen bauta masa shi kaxai, ku bi umarnin da na yi muku, kar ku bauta wa wani koma bayansa".**

**(91) Waxanda suka fitinu da bautan xan maraqi suka ce: "Ba zamu gushe akan bautarsa ba har sai Musa ya dawo wurinmu".**

**(92) Annabi Musa (A.S) ya ce wa xan 'uwansa Annabi Haruna (A.S): "Mai ya hana ka lokacin da ka ga sun vace ta hanyar bautar xan Maraqi".**

**(93) Ka bar su ka same ni?! Ko ka sava wa umarni na ne, yayin da na sa ka halifa a cikinsu?!.**

**(94) Yayin da Annabi Musa (A.S) ya kama gemun xan 'uwansa yana jan shi zuwa gare shi, yana mai inkarin abin da ya aikata, sai Annabi Haruna yace masa, ya na neman ya tausaya masa: "Kada ka kama gemuna ko gashin kaina, ina da uzurin tsayawa tare da su, don na ji tsoron in na tafi na barsu su kaxai, su rarrabu, kai kuma ka zo ka ce, na raba tsakaninsu, ban kiyaye wasiyyar da ka yi min a kansu ba".**

**(95) Annabi Musa (A.S) ya ce wa Samiriyyu: "Mene ne ya same ka, ya kai Samiriyyu? Me ya kai ka aikata wannan abin da ka yi?".**

**(96) Samiriyyu yace wa Annabi Musa (A.S): "Na ga abin da ba su gani ba ne, na ga Mala'ika Jibrilu ne a kan Doki, sai na xauki jimqin qasa guda xaya na sawun Dokinsa, sai na jefa shi akan narkakken zinarin da ake qera shi akan kamannin xan maraqi, sai ya zama xan maraqi yana kuka. Haka zuciya ta ta qawata mini abin nan da na aikata".**

**(97) Annabi Musa (A.S) ya ce wa Samiriyyu: "Je ka amma matuqar kana raye zaka riqa cewa: "Ba zan shafi kowa ba, kuma ni ma ba za a shafe ni ba". Zaka rayu a wulaqance. Kuma akwai wani lokaci a ranar alqiyama da za a yi maka hisabi a cikinsa, a yi maka uquba. Allah ba zai sava maka wannan alqawarin ba. sannan ka kalli xan maraqinka da ka xauke shi abin bautarka, ka tsaya akan bautarsa koma bayan Allah, zamu kunna masa wuta har sai ya narke, sannan zamu warwatsa shi a cikin teku har ya zama babu abin zai rage.**

**(98) Kaxai abin bautarku na gaskiya – Ya ku mutane - shi ne Allah, wanda babu wani abin bauta da cancanta sai shi, iliminsa ya kewaye komai. Babu wani abu wanda yake kuvuce wa iliminsa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Yaudarar mutane ta hanyar canza haqiqanin abubuwa daga yadda suke, hanya ce ta vatattu.**
**2 - Fushin da ake yabo shi ne wanda aka yi don an keta alfarmar abubuwan da Allah ya haramta.**
**3 - A cikin ayoyin akwai dalili akan halaccin korar 'yan bidi'a da masu savo, da qaurace musu, da rashin cuxanya da su. 4 - A cikin ayoyin akwai wajabcin yin tunani don sanin Allah Maxaukakin Sarki, ta hanyar ayyukansa da ya halitta a duniya .**

كَذَٰلِكَ نَقُصُّ عَلَيْكَ مِنْ أَنۢبَآءِ مَا قَدْ سَبَقَ ۚ وَقَدْ ءَاتَيْنَٰكَ مِن لَّدُنَّا
ذِكْرًا ﴿٩٩﴾ مَّنْ أَعْرَضَ عَنْهُ فَإِنَّهُۥ يَحْمِلُ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ وِزْرًا
﴿١٠٠﴾ خَٰلِدِينَ فِيهِ ۖ وَسَآءَ لَهُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ حِمْلًا ﴿١٠١﴾ يَوْمَ يُنفَخُ
فِى ٱلصُّورِ ۚ وَنَحْشُرُ ٱلْمُجْرِمِينَ يَوْمَئِذٍ زُرْقًا ﴿١٠٢﴾ يَتَخَٰفَتُونَ
بَيْنَهُمْ إِن لَّبِثْتُمْ إِلَّا عَشْرًا ﴿١٠٣﴾ نَّحْنُ أَعْلَمُ بِمَا يَقُولُونَ إِذْ يَقُولُ
أَمْثَلُهُمْ طَرِيقَةً إِن لَّبِثْتُمْ إِلَّا يَوْمًا ﴿١٠٤﴾ وَيَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلْجِبَالِ
فَقُلْ يَنسِفُهَا رَبِّى نَسْفًا ﴿١٠٥﴾ فَيَذَرُهَا قَاعًا صَفْصَفًا ﴿١٠٦﴾
لَّا تَرَىٰ فِيهَا عِوَجًا وَلَآ أَمْتًا ﴿١٠٧﴾ يَوْمَئِذٍ يَتَّبِعُونَ ٱلدَّاعِىَ
لَا عِوَجَ لَهُۥ ۖ وَخَشَعَتِ ٱلْأَصْوَاتُ لِلرَّحْمَٰنِ فَلَا تَسْمَعُ إِلَّا هَمْسًا
﴿١٠٨﴾ يَوْمَئِذٍ لَّا تَنفَعُ ٱلشَّفَٰعَةُ إِلَّا مَنْ أَذِنَ لَهُ ٱلرَّحْمَٰنُ وَرَضِىَ لَهُۥ
قَوْلًا ﴿١٠٩﴾ يَعْلَمُ مَا بَيْنَ أَيْدِيهِمْ وَمَا خَلْفَهُمْ وَلَا يُحِيطُونَ بِهِۦ
ثلاثة أرباع الحزب ٣٢ عِلْمًا ﴿١١٠﴾ ۞ وَعَنَتِ ٱلْوُجُوهُ لِلْحَىِّ ٱلْقَيُّومِ ۖ وَقَدْ خَابَ مَنْ حَمَلَ
ظُلْمًا ﴿١١١﴾ وَمَن يَعْمَلْ مِنَ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَهُوَ مُؤْمِنٌ فَلَا يَخَافُ
ظُلْمًا وَلَا هَضْمًا ﴿١١٢﴾ وَكَذَٰلِكَ أَنزَلْنَٰهُ قُرْءَانًا عَرَبِيًّا وَصَرَّفْنَا
فِيهِ مِنَ ٱلْوَعِيدِ لَعَلَّهُمْ يَتَّقُونَ أَوْ يُحْدِثُ لَهُمْ ذِكْرًا ﴿١١٣﴾



**(99) Kamar yadda Muka baka labarin Annabi Musa da Fir'auna da mutanensu – Ya kai wannan Manzo - haka muke baka labarin waxanda suka wuce gabaninka na Manzanni, da al'ummu daban daban, don ya zama lallashi gare ka. Kuma tabbas mun baka abin karantawa daga wurinmu, wanda mai wa'azantuwa yake wa'azantuwa da shi.**
**(100) Duk wanda ya kau da kai daga wannan Alqur'anin da aka saukar maka da shi, ya qi yin imani da shi, ya qi yin aiki da abin da yake cikinsa, to lallai zai zo a ranar alqiyama yana xauke da babban laifi, yana mai cancantar uquba mai raxaxi akan hakan. (101) Za su zauna cikin wannan azaba har abada, kuma tir da wannan nauyin da suke xauke da shi a ranar alqiyama.**
**(102) Ranar da Mala'ika zai busa qaho busa ta biyu, don tashi bayan mutuwa, kuma zamu tara kafirai a wannan ranan, launinsu da idanunsu zasu zama korara shar, saboda abin da zasu gamu da shi na tsananin abubuwan ban tsoro na lahira.**
**(103) Suna yi wa junansu raxa, suna cewa: "Ba wani zama kuka yi ba a barzahu, bayan mutuwarku, face dare goma kawai". (104) Mune mafi sanin abin da suke raxawa junansu, babu abin da yake vuya gare mu a cikinsa, yayin da mafi hankalin cikinsu yake cewa: "Ba ku zauna a barzahu ba, face yini xaya kacal, ba qari".**
**(105) Suna tambayar ka – Ya kai wannan Manzo – Dangane da halin da duwatsu za su kasance a ciki ranar alqiyama, to ka ce da su: "Ubangijina zai tunbuqe su daga can qasansu, ya sheqe su, su zama toka".**
**(106) Ya bar qasar da suke kai fili, babu gini ko wani tsiro a bayanta. (107) Ba zaka ga wata kwana ko wani tudu ko gangara a kan qasar ba – Ya kai mai kallo - saboda tsananin daidaiton ta.**
**(108) A wannan ranar, mutane za su bi muryar mai kira zuwa filin taron alqiyama, babu wanda zai kawar da su daga bin sa, muryoyin kuma sun yi shiru don tsoron Allah mai rahama, ba za ka ji wani sauti a ranar ba, sai can qasa a voye. (109) A wannan rana mai girma, ceton wani mai ceto ba zai yi amfani ba, sai dai mai ceton da Allah ya yi masa izinin ya yi ceton, kuma ya yarda da zancensa wacen neman ceton. (110) Allah tsarki ya tabbata a gare shi, ya san abin da mutane ke fuskanta na al'amrin tashin alqiyama. Kuma ya san abin da suka bari a baya a duniyarsu, Kuma bayi gaba xayansu ba za su iya kewaye sanin zatin Allah da siffofinsa ba. (111) Fuskokin bayi za su qasqantar da kai, su miqa wuya ga Allah, rayayyen da baya mutuwa, wanda yake tsaye akan lamarin bayinsa, ta hanyar gudanar da su da jujjuya su. Kuma tabbas duk wanda ya xauki kayan savo ya yi hasara, saboda ya kai kansa wuraren halaka. (112) Duk wanda ya yi aiki nagari, yana mai imani da Allah da manzanninsa, to zai samu sakamakonsa cikakke, kada ya ji tsoron wani zalunci, na a yi masa azaba akan zunubin da bai aikata shi ba, ko a rage masa ladan wani aikin nagari da ya yi. (113) Kuma kamar yadda muka saukar da labarin magabata, haka muka saukar da wannan Alqur'ani da harshen Larabci bayyananne, kuma muka bayyana dangogin gargaxi na tsawatarwa da tsoratarwa, da fatan zasu ji tsoron Allah, ko kuma Alqur'ani ya haifar musu da wani wa'azi ko izina.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Alqur'ani mai girma gaba xayansa tunatarwa ne da wa'azi ga al'ummu da jama'a da xaixaikun mutane, kuma xaukaka ne da abin alfahari ga jinsin mutum. 2 - Ceto ba zai amfani kowa ba, sai dai ceton wanda Allah mai rahama ya yi masa izini, kuma ya yarda da zancensa na neman ceton. 3 - Alqur'ani ya qunshi mafi kyawun hukunce-hukunce, waxanda hankali da xabi'a sun bayar da shaida akan kyawunsu da cikarsu. 4 - Yana daga cikin ladubban mu'amala da Alqur'ani a qarve shi da yarda, da miqa wuya, da girmamawa, da shiryuwa da haskensa zuwa tafarki madaidaici, da fuskantarsa da koyo da koyarwa. 5 - Nadamar masu laifi a ranar lahira a dalilin kasancewarsu sun vata lokaci mai yawa, sun tafiyar da shi suna masu wargi da rafkana, da kauce wa abin da zai amfanesu, da fuskantar abin da zai cuce su.**

فَتَعَٰلَى ٱللَّهُ ٱلۡمَلِكُ ٱلۡحَقُّۗ وَلَا تَعۡجَلۡ بِٱلۡقُرۡءَانِ مِن قَبۡلِ أَن
يُقۡضَىٰٓ إِلَيۡكَ وَحۡيُهُۥۖ وَقُل رَّبِّ زِدۡنِي عِلۡمٗا ١١٤ وَلَقَدۡ عَهِدۡنَآ
إِلَىٰٓ ءَادَمَ مِن قَبۡلُ فَنَسِيَ وَلَمۡ نَجِدۡ لَهُۥ عَزۡمٗا ١١٥ وَإِذۡ قُلۡنَا
لِلۡمَلَٰٓئِكَةِ ٱسۡجُدُواْ لِأٓدَمَ فَسَجَدُوٓاْ إِلَّآ إِبۡلِيسَ أَبَىٰ ١١٦
فَقُلۡنَا يَٰٓـَٔادَمُ إِنَّ هَٰذَا عَدُوّٞ لَّكَ وَلِزَوۡجِكَ فَلَا يُخۡرِجَنَّكُمَا
مِنَ ٱلۡجَنَّةِ فَتَشۡقَىٰٓ ١١٧ إِنَّ لَكَ أَلَّا تَجُوعَ فِيهَا وَلَا تَعۡرَىٰ
١١٨ وَأَنَّكَ لَا تَظۡمَؤُاْ فِيهَا وَلَا تَضۡحَىٰ ١١٩ فَوَسۡوَسَ إِلَيۡهِ
ٱلشَّيۡطَٰنُ قَالَ يَٰٓـَٔادَمُ هَلۡ أَدُلُّكَ عَلَىٰ شَجَرَةِ ٱلۡخُلۡدِ وَمُلۡكٖ
لَّا يَبۡلَىٰ ١٢٠ فَأَكَلَا مِنۡهَا فَبَدَتۡ لَهُمَا سَوۡءَٰتُهُمَا وَطَفِقَا
يَخۡصِفَانِ عَلَيۡهِمَا مِن وَرَقِ ٱلۡجَنَّةِۚ وَعَصَىٰٓ ءَادَمُ رَبَّهُۥ فَغَوَىٰ
١٢١ ثُمَّ ٱجۡتَبَٰهُ رَبُّهُۥ فَتَابَ عَلَيۡهِ وَهَدَىٰ ١٢٢ قَالَ ٱهۡبِطَا مِنۡهَا
جَمِيعَۢاۖ بَعۡضُكُمۡ لِبَعۡضٍ عَدُوّٞۖ فَإِمَّا يَأۡتِيَنَّكُم مِّنِّي هُدٗى
فَمَنِ ٱتَّبَعَ هُدَايَ فَلَا يَضِلُّ وَلَا يَشۡقَىٰ ١٢٣ وَمَنۡ أَعۡرَضَ
عَن ذِكۡرِي فَإِنَّ لَهُۥ مَعِيشَةٗ ضَنكٗا وَنَحۡشُرُهُۥ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ
أَعۡمَىٰ ١٢٤ قَالَ رَبِّ لِمَ حَشَرۡتَنِيٓ أَعۡمَىٰ وَقَدۡ كُنتُ بَصِيرٗا ١٢٥



**(114) Allah ya xaukaka, ya tsarkaka, ya girmama, shi mai mulkin da ya mallaki komai, wanda shi ne gaskiya, zancensa ma gaskiya, ya xaukaka daga barin abin da mushirikai suke siffata shi da shi. Kada ka yi gaggawa – Ya kai wannan Manzo-cikin karatun Alqur'ani tare da Mala'ika Jibril, tun kafin ya gama isar maka da shi. Kuma ka ce: "Ya Ubangijina ka qara min ilimi, qari akan ilimin da ka bani". Yayin da Allah ya ambaci qissar Annabi Musa (A.S) da abin da ta qunsa na bijirewar Fir'auna da gafalar Bani Isr'ila, sai ya ambaci qissar Annabi Adam (A.S) domin kwaxaitar da wanda ya manta ya koma zuwa ga biyayya ga Allah, ya ce: (115) Haqiqa mun yi wa Annabi Adam (A.S) wasiyya da kar ya ci daga wannan bishiyar, mun hana shi yin hakan, kuma mun bayyana masa sakamakon hakan, amma sai ya manta da wasiyyar ya ci daga bishiyar, bai yi haqurin barinta ba, kuma bamu ga qarfin azamar kiyaye abin da muka yi masa wasiyya da shi daga wurinsa ba. (116) Ka tuna – Ya kai wannan Manzo-yayin da muka cewa Mala'iku: "Ku yi sujjadar gaisuwa ga Annabi Adam (A.S), sai suka yi masa sujjada dukkaninsu, banda Iblis – wanda ya kasance tare da su amma ba xaya daga cikinsu ba ne shi - ya qi ya yi sujjada saboda girman kai.**
**(117) Sai muka ce: "Ya kai Adam, lallai Iblis abokin gabarka ne, abokin gabar matarka ne, kar ku sake ya fitar da ku, kai da matarka daga Aljanna, ta hanyar yi masa biyayya cikin abin da zai yi muku waswasi da shi, don kai ne zaka sha wahala in hakan ta faru.**
**(118) Lallai kana da alqawarin Allah na ya ciyar da kai a Aljanna, ba zaka ji yunwa ba, kuma ya tufatar da kai, ba za ka yi tsiraici ba. (119) Kuma ya shayar da kai, ba zaka ji qishi ba, kuma ya yi maka inuwa, ba zaka ji zafin rana ba.**
**(120) Sai Shaixan ya yi wa Annabi Adam waswasi, ya ce masa: "Shin in nuna maka wata bishiya wadda duk wanda ya ci daga gare ta ba zai mutu ba har abada, zai wanzu, ya zauna da rayuwarsa, kuma ya yi mulki mai xorewa, wanda ba zai yanke ko ya qare ba?!" (121) Sai Annabi Adam da Hauwa suka ci daga bishiyar da aka hana su cinta, sai al'aurarsu ta bayyana a gare su bayan ta kasance a suturce, suka fara tsinkar ganyen bishiyoyin Aljannah, suna rufe al'aurarsu da su. Annabi Adam ya sava wa umarnin Ubangijinsa yayin da bai bi umarnin da ya yi masa na nesantar ci daga bishiyar nan ba, ya qetare iyaka zuwa ga abin da bai halatta masa ba.**
**(122) Sannan sai Allah sai ya zave shi, ya karvi tubansa, ya yi masa dace da shiriya.**
**(123) Allah yace wa Adam da Hauwa: "Ku sauka daga Aljannah ku biyun tare da Iblis, shi abokin gabarku ne, ku ma abokan gabarsa ne. Idan wani bayani na shiriya zuwa ga tafarkina yazo muku, to duk wanda a cikinku ya yi biyayya ga shiriya ta, ya yi aiki da ita, bai kauce ba, to ba zai vata daga kan gaskiya ba, kuma ba zai sha wahalar azaba a lahira ba, Allah zai shigar da shi Aljannah. (124) Duk wanda kuma ya juya wa ambatona baya, yaqi ya karve shi, yaqi ya amsa kiransa, to yana da rayuwar qunci a gidan duniya da rayuwr barzahu, kuma zamu tasa qeyarsa zuwa filin taron alqiyama yana makaho, maras ido, maras basira. (125) Sai wannan da ya juya baya ga ambatona yana cewa: "Ya Ubangijina saboda me ka tayar da ni makaho alhali a duniya na kasance mai gani ne ni?"**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Yin ladabi wajen koyon ilimi, kuma mai sauraron ilimi ya dace ya bi sannu sannu, ya yi haquri, har mai yin shifta ko malami ya qare zancensa, wanda sashensa yake da alaqa da sashe. 2 - Annabi Adam ya yi mantuwa sai zuriyarsa ma suka zama masu mantuwa, bai tabbata akan azama mai qarfi ba, su ma haka suke, kuma ya yi saurin tuba sai Allah ya gafarta masa, duk wanda ya yi kama da babansa to bai yi zalunci ba. 3 - Falalar tuba, saboda Annabi Adam (A.S) ya kasance mafi falala bayan tubansa, sama da yadda yake kafin ya tuba. 4 - Rayuwar qunci a gidan duniya da barzahu da lahira ta tabbata ga kafirai da vatattu.**

قَالَ كَذَٰلِكَ أَتَتۡكَ ءَايَٰتُنَا فَنَسِيتَهَاۖ وَكَذَٰلِكَ ٱلۡيَوۡمَ تُنسَىٰ ١٢٦
وَكَذَٰلِكَ نَجۡزِي مَنۡ أَسۡرَفَ وَلَمۡ يُؤۡمِنۢ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِۦۚ وَلَعَذَابُ ٱلۡأٓخِرَةِ
أَشَدُّ وَأَبۡقَىٰٓ ١٢٧ أَفَلَمۡ يَهۡدِ لَهُمۡ كَمۡ أَهۡلَكۡنَا قَبۡلَهُم مِّنَ ٱلۡقُرُونِ
يَمۡشُونَ فِي مَسَٰكِنِهِمۡۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّأُوْلِي ٱلنُّهَىٰ ١٢٨
وَلَوۡلَا كَلِمَةٞ سَبَقَتۡ مِن رَّبِّكَ لَكَانَ لِزَامٗا وَأَجَلٞ مُّسَمّٗى ١٢٩
فَٱصۡبِرۡ عَلَىٰ مَا يَقُولُونَ وَسَبِّحۡ بِحَمۡدِ رَبِّكَ قَبۡلَ طُلُوعِ ٱلشَّمۡسِ
وَقَبۡلَ غُرُوبِهَاۖ وَمِنۡ ءَانَآيِٕ ٱلَّيۡلِ فَسَبِّحۡ وَأَطۡرَافَ ٱلنَّهَارِ لَعَلَّكَ
تَرۡضَىٰ ١٣٠ وَلَا تَمُدَّنَّ عَيۡنَيۡكَ إِلَىٰ مَا مَتَّعۡنَا بِهِۦٓ أَزۡوَٰجٗا مِّنۡهُمۡ زَهۡرَةَ
ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا لِنَفۡتِنَهُمۡ فِيهِۚ وَرِزۡقُ رَبِّكَ خَيۡرٞ وَأَبۡقَىٰ ١٣١ وَأۡمُرۡ أَهۡلَكَ
بِٱلصَّلَوٰةِ وَٱصۡطَبِرۡ عَلَيۡهَاۖ لَا نَسۡـَٔلُكَ رِزۡقٗاۖ نَّحۡنُ نَرۡزُقُكَۗ وَٱلۡعَٰقِبَةُ
لِلتَّقۡوَىٰ ١٣٢ وَقَالُواْ لَوۡلَا يَأۡتِينَا بِـَٔايَةٖ مِّن رَّبِّهِۦٓۚ أَوَلَمۡ تَأۡتِهِم
بَيِّنَةُ مَا فِي ٱلصُّحُفِ ٱلۡأُولَىٰ ١٣٣ وَلَوۡ أَنَّآ أَهۡلَكۡنَٰهُم بِعَذَابٖ
مِّن قَبۡلِهِۦ لَقَالُواْ رَبَّنَا لَوۡلَآ أَرۡسَلۡتَ إِلَيۡنَا رَسُولٗا فَنَتَّبِعَ
ءَايَٰتِكَ مِن قَبۡلِ أَن نَّذِلَّ وَنَخۡزَىٰ ١٣٤ قُلۡ كُلّٞ مُّتَرَبِّصٞ فَتَرَبَّصُواْۖ
فَسَتَعۡلَمُونَ مَنۡ أَصۡحَٰبُ ٱلصِّرَٰطِ ٱلسَّوِيِّ وَمَنِ ٱهۡتَدَىٰ ١٣٥



**(126) Allah maxaukakin Sarki ya ce, yana mai masa raddi: "Irin haka ka yi a duniya, tabbas ayoyinmu sun zo maka, amma sai ka kawar da kai, ka qyalesu. To haka kai ma za a qyale ka yau cikin azaba". (127) Irin wannan sakamakon ne muke saka wa duk wanda ya dulmiya cikin sha'awar abubuwan da aka haramta, ya kawar da kai daga yin imani da dalilai bayyanannu daga wurin Ubangijinsa. Kuma lallai azabar Allah a lahira ita ta fi tsananin firgitarwa da wanzuwa sama da quncin rayuwar gidan duniya da na barzahu. (128) Shin mushirikai ba su da masaniyar yawan al'ummun da muka halakar da su gabaninsu ne, alhali suna yawo a wuraren waxancan al'ummun da aka halakar, suna ganin ragowar abin da ya faru da su? Lalli akwai abin izina ga masu hankali cikin abin da ya faru da waxancan al'ummu masu yawa na halaka. (129) Ba don maganar da ta riga ta gabata daga Ubangijinka ba – Ya kai wannan Manzo - na cewa ba zai azabtar da wani kafin a tsayar da hujja a kansa ba, kuma ba don wani ajali qayyadadde da ya zana a wurinsa ba, da ya gaggauta musu azaba, saboda sun cancanci hakan. (130) Amma ka yi haquri – Ya kai wannan Manzo-akan abin da masu qaryata ka suke faxa na siffofin vaci, kuma ka yi tasbihi da godiya ga ubangijinka a cikin sallar alfijir, gabanin vullowar rana, da a cikin sallar Azzahar a lokacin zawali, lokacin da rabin farkon yini ya wuce, da sallar magariba bayan rabi na biyu na yini ya wuce, don fatan ka samu irin ladan da za ka yi farin ciki, ka yarda da shi, a wurin Allah. (131) Kuma kar ka kalli abin da muka sanyawa vangarorin waxannan masu qaryata Annabawa a matsayin xan jin daxi da suke gwangwajewa da shi na qawar rayuwar duniya, don mu jarraba su da shi. Lallai abin da muka sanya musu na wannan xin mai gushewa ne. Amma ladan Ubangijinka wanda ya yi maka alqawarinsa har sai ka yarda da shi ya fi alheri da wanzuwa, don ba ya yankewa, kuma yana sama da abin da muka ba su na jin daxin rayuwar duniya mai qarewa. (132) Ka umarci iyalanka – Ya kai wannan Manzo- su tsayar da sallah, kuma kai ma ka xore wajen tsayar da ita, ba zamu tambayeka – kai ko wannika - wata dukiya ba, saboda yin sallah. Mune masu azurta ka. Kuma kyakkyawan qarshe a duniya da Lahira yana ga masu taqawa, waxanda suke jin tsoron Allah, suke aikata umarninsa, suna nisantar haninsa. (133) Waxannan kafirai masu qaryata Annabi (S.A.W) za su ce: "Me ya sa Muhammadu ba zai zo mana da wata alama daga wurin Ubangijinsa ba, wadda zata nuna gaskiyarsa da kuma cewa shi Manzo ne. Shin Alqur'ani, wanda yake gasgata littattafan da suka gabata, bai zo musu ba ne?. (134) Da mun halaka waxannan masu qaryata Annabi (S.A.W) ta hanyar saukar musu da wata azaba, saboda kafircinsu da taurin kunnensu gabanin mu aiko musu da Manzo, mu saukar musu da littafi, da sun ce: "Ina ma da – Ya Ubangijinmu - ka aiko mana da Manzo a duniya!. Da mun yi imani, mun bi abin da ya zo da shi na ayoyi, kafin tavewa da wulaqanci su afka mana ta hanyar azabarka?! (135) Ya kai wannan Manzo, ka cewa waxannan masu qaryata Manzannin: "Kowanne daga cikinmu – mu da ku - fa yana jiran abin da Allah zai gudanar ne. To ku saurara, lallai da sannu zaku sani -babu makawa - su waye ma'abota tafarki madaidaici, kuma su wanene shiyayyu: Mu ko kuma ku?.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Yana daga cikin hanyoyin da suke taimakawa wajen jurewa cutarwar masu kawar da kai daga ayoyin Allah, ribatar lokuta masu falala wajen yin tasbihi da godiya ga Allah. 2 - Ya dace ga bawa idan ya lura da karkatar zuciyarsa da sha'awarsa zuwa ga adon duniya ya auna tsakanin adon duniyar mai gushewa, da ni'imar lahira mai dauwama, ya gani. 3 - Wajibi ne akan bawa ya tsayar da sallah iyakar tsayarwa, kuma idan wani abu ya dame shi, to ya tashi ya yi sallah, ya umarci iyalansa su yi salla, kuma ya yi haquri da su, don koyi da Manzon Allah (S.A.W). 4 - Kyakkyawar makoma abin yabo wadda ita ce Aljanna ta masu taqawa ce.**